Ajiye spoon din hannunsa yayi ahankali Yana kallan Sayd din yace

"Mama ta hadu tsautsayi haka me yasa baa fadamun ba?
Akwai wani dalilin qin fadamun ne?

Shiru dukkaninsu sukai sbd ganin yanda ransa ya baci da yanda kuma bacin ran da fushi yake a bayyane.

Sake maimaita tambayarsa yayi cikin fada wadda ta saka Sayd cewa

"Baka kusa ne shiy.....

"Unbelievable" ya fada yana katse Sayd din tareda miqewa Yabar dining din falaq ta bisa da kallo cikeda mamakin ganin fushin daddynta da duk abinda zakai masa baka iya ganin fushinsa a bayyane.

Sayd kuwa daya San ba qaramin abu ke fidda fsuhin AZIZ dinba dan haka maganar Mama bata kai sakasa wannan mummunan bacin ran d fushin ba.

Mama data fito daga dakinta cikin dauriya da dannewa sbd batason ciwon yayi nauyin da AZIZ zai nema bin dalilin yawan rauninta a kwanakin dan haka ta lallabo ta fito sbd cin abinci a cikinsu ko yayane sai gashi tana kawowa kunnuwanta suka jiyar mata fadansa da tashin muryansa data sake tabbatarda matsayinta a gurinsa Yama wuce yanda take tinanin yayi sanyi sbd Soyayyar Jannah dan haka kai tsaye ta juya tana jin sanyi na mamaye ranta,

Idan har ransa zai mummunan baci hakan to tabbas ita babu ma abinda take buqata a yanzu bayan ganin ta rabasa da Jannah sbd idan ta rabasa da itane zai nesanta da Zaadens su qara tsanar junan da zasu zabi nesa nesa da juna su bace a rayuwarsu da Fatima gbaki daya,

Abinda ta tabbatar a yanzu shine idan bata nesanta kanta da Fatima ba Fatima zata iya ajalinta sbd idan ta sake mata irin wannan dukan zata iya rasa ranta ko wani sashen na jikinta dan haka idan har bazata iya korar zaadens su tafi su fita rayuwarsu da Fatiman ba sbd AZIZ ya saka dokar babu me barin 4&4 sedai izininsa to tabbas shi datake da cikakken iko dashi zata sake tabbatar masa da bata yafe ya sake ko kallan Jannah ba bare Zaadens,

A baya ta fada masa baya yadda ko yafe ya sake ambatar ko sunan Jannah da bakinsa ba Wanda kuma ta tabbatarda hakan dan kuwa har yau bakinsa bai taba sake furta sunan Jannah ba.

Idan duk yanda taso ta kasa yiyuwa zata juya danta da shine takeda cikakken ikonsa.

Ko daya iso saman kai tsaye dakinta ya nufa tareda miqa hannu yayi knockin a natse kafin ya bada seconds tukuna ya bude dakin bakinsa dauke da sallama.

Zaune take Maman a bakin gado ta dago tana kallansa da yanayi na sanyi da rashin cikakkiyar lafiya.

Qarasowa yayi ya zauna a sofa Yana dagowa cikin nutsuwa shima ba wata sakewa har lokacin a fuskansa yanayinsa na fushin da zuciyarsa take ciki a dan bayyane dan itama maman kai tsaye tana kallansa ta gano hakan zuciyarta ta sake cikewa da jin dadin ganin damuwa da bacin ransa akan ciwonta.

Gaidata yayi cikin kulawa ya Dora da cewa

"Yaya jikin?
Ko zaa sake Kiran likita ya dubaki ne?
Kokuma Mama zaa gyara Miki sabon daki ne a qasa ki koma sbd stairs dinnan kaman sun fara damunki"

Girgiza kai tayi tana bude baki tace

"Aa ba buqatan hakan tsautsayi ne kawai da zuwan lamari"

"Allah ya tsare gaba Mama"

"Amin" tace tana gyara zama ta kallesa kai tsaye tace

"AZIZ a yanzu da Zaadens suke gida daya a tareda mu duk da a karkashinmu suke kuma suna matsayin masu aikinmu ne inason sake tinatar dakai alkawarin dayake Kanka akansu,
AZIZ Ni mahaifiyarka ina Nan kan bakana ban yadda ba ban aminta ba idan har da gaske nice uwa a gareka ka kulasu ko basu wata kulawa ko sabuwar fuskar data wuce matsayinsu na masu aiki da suke dashi,

Ban Aminta da kowace irin muamala a tsakaninka dasu ba hakama ban Aminta ko inda Jannah take ka sake kalla ba idan ba hakan ba kuwa sedai ka zaba ko su ko ni nabar gidan nakoma kauye,

Zabi Yana gurinka a tsakanin mahaifiyarka da kuma Wanda suka kashe kanwarka suka raya tasu Yar"

Tinda ta fara magana bai dagoba ya kalleta sai datakai karshe ya dago idanuwansa ya kalleta,

Magana yaso yi akan cikakken aurensa dayake kan Jannah din da tin daga ranar data sakasa alkawarin rashin sake ambatar sunanta bai sake ambatar sunan ba Sedai 4&4 daya saka mata wanda bayan Sayd babu Wanda yasan maanarsa,

Wani abu me nauyi da zafi ya hadiye a moqoshinsa zuwa kirjinsa kafin ya hadiye maganar ya fasa fada sbd auren dai ba mutuwa zeyiba koda hakan na nufin rasa rayuwarsa ne bazai iya bawa kowa 4&4 ba koda mahaifinta daya haifeta ne kuwa hakama shi kansa idan har kowa na tinanin aurensa da ita ya qare tintini baya buqtaan fadawa kowa da bakinsa lokaci duka zai bayyanarwa da kowa kaman yanda ya zabi ya bata lokaci ta sauko daga fushinta ita kanta Jannah din sbd a yanzu iya tsanarsa ce kawai yake gani a tattare da ita wadda hakan ze iya kashesa daga tsaye.

Miqewa yayi ya fice daga dakin Maman tabisa da kallo tana sauke ajiyan zuciya sbd ta hakan dai tasan zai bawa Zaadens baya koma kila ya bari a basu damar tafiyarsu ta yanda komai zai

tafi mata a daidai,

Koda basu tafi a kusa ba tasan dai yanzu zai dauke idanuwansa kwata kwata daga Zaadens ita kuma zata saka Sisi tsananta tsoron hana Fatima fitowa koina duk rintsi kafin ta samu hanyar fiddasu daga gidan.

Yana saukowa kai tsaye fita yayi bayan ya bada umarnin a gyara samansa.

Mota ya dauka ya fice daga gidan gabaki daya.

Fiddausi ce tahau saman da kanta taga aikin sosai ne sbd glasses koina dan haka ta kira Fatma sbd Jannah a gurinsu har abada ta wuce zama Yar aiki.

A gurin gyaran Fatma ce idanuwanta suka fara sauka akan bra din Jannah dake yashe a tsakiyar dakin ta dago a sace zata kalli fiddausi wadda itama ta gani tin dazu ta kasa cewa komai.

Cikin sanyi Fatma ta dauke bra din ta dauke hadda rigar suka qarasa gyra koina suka fito.

Fatma na wucewa itama fiddausi sama ta nufa tana Kiran Sayd ta sanar dashi ba mirror na dresser da Ctable na dakin AZIZ din sbd a kawo wasu gobe.

Fatma na zuwa da kayan hannunta dakinsu takai batareda ta bari su Dad da kowa dake zaune ana dan fira b sun gani tukuna ta dawo ta zauna cikinsu ana yi da ita.

*******Washe gari a gidan kowa fes ya tashi da sabon kudirin daya daukanwa Kansa,

ZAADENs dai suna Nan akan bakansu babu har abada abinda zai sake hadasu da LIMBA,

Hakama maganar auren Jannah da Ammar ba fashi Dad ya fada ya tabbatar hakama Maheer dan haka Ammar ya samu karfin gwiwan gaske Musamman ganin Jannah din kanta shi take so shi ta zaba,

Ita kanta Jannah batajin akwai sauyi a kudirinta na rabuwa da aurensa batareda ma kowa yasan akwai auren ba hakama babu sauran muamala a tsakaninta dashi bayan ta matsayinsa na Boss a gareta da familynta.

A bangaren fatma ma tayi shiru babu alaman tasan komai ma sbd kada su Dad su gano kaman yanda Jannah tace batason kowa ya Sani dan haka zata tayata boye dukkanin sirrin dayake tsakaninta da AZIZ.

****AZIZ LIMBA da kansa ma ya daukewa kowa dayake gidan sbd gabaki daya Yama dena zama ya saka kansa zama busy sosai,

Kwata kwata ya dena saukowa dining sbd da safe yake fita da dare yake dawowa.

Hakan yayiwa Mama daidai yanda takeso dan haka ta warke ta saki jikinta tana komawa huldodinta da Nicky wadda itama sai datai kwana biyu kafin ta dawo cikakken hayyacinta.

Ticket da komai na komawa AZIZ yayi mata ta tashi zarewa saida Mama ta dakatar da tafiyar tareda sake tada maganar aurensa da Nicky din.

Duk lokacinda ya bawa Jannah na rage fushinta bai alaman hakan zai yiyuwa bayan a nasa bangaren a cikin azaba yake rayuwa a yanzu,

Rashin ganinta kadai ya saka lafiyansa na neman gagaransa hakama a tsakaninsa dasu Dzad kwata kwata babu wata fuska ko alaman akwai sassaucin gaba da tsanar da suke ciki sbd ko kallansa basa kaunar yi kaman yanda shima haryanxu ya kasa jinsu ko kadan a zuciyarsa,

Jannah kawai yake son,ita kadai yake buqata,itace lafiya da warakar da kawai yake nema a wannan rayuwar tasa da rashin Ummansa da Ummitah suka birkitata.

Nicky wadda yau ta fita tareda Ammar wanda ta sakar masa fuska Amma shi bai sauya daga yanda yake ba ba sakewa a tsakaninsu..

Sai yamma sosai suka dawo gida har ta fice motar ta dawo ta bude jakar hannunta ta miqa masa robar Soft drink na pineapple tace

"Ina fatan abinda duk ya faru ya wuce"

Gyada kai kawai yayi batareda ya kalleta ba ya karba ya wucewansa.

Yana gap da isa dakinsu ya hadu da fatma ya jefa mata Yana cewa

"Ki bawa wani Ni bana Sha"

Cikin dariya fatma tace

"Nagode ya Ammar"

Kitchen zata dan haka ta shiga daki ta ajiye ta fice zuwa kitchen.

Jannah dake toilet tana fitowa daga wanka ummah na shigowa dakin ta zauna tana cewa

"Ruwa zansha"

Cikin kulawa Jannah tace

"Ummah ba ruwa a dakin Nan amma bara na shirya naje na dauko Miki kinji Umman Jan"

Girgiza kai Umman tayi idanuwanta n sauka kan soft drink din ta miqa hannu ta dauka tareda bawa Jannah tace ta bude mata.

Turaren hannunta Jannah ta ajiye tana karba ta bude mata tana cewa

"Fatma ta ajiyesa kisha idan naje kitchen na dauko mata wani"

Budewa tayi ta bawa Umman ta karba ahankali takai bakinta Tasha ta sake Sha taji bai mata dadiba dan haka ta miqawa Jannah din tana cewa

"Na koshi bana Sha"

Karba Jannah tayi cikin sauri ta qasara shanyewa ta ajiye robar tana saka hijab kan kayanta ta fice sbd aikin data bari kitchen.

Nicky wani irin farin ciki da nutsuwa ta samu tana jin ayau matsalarta data Mama zata kau sbd matiqar Ammar yasha abinda ta basa ayau bazai kwana ba saiya haiqewa Jannah wanda ko bai haiqewa Jannah ba to zata yanda zatai ta tura Falaq can ya haiqe mata ta yanda AZIZ zai tsani Zaadens tsana mafi muni idanma bai illatasu gabaki dayansu ba.

Kallan mama tayi bayan ta gama jero mata bayanin komai ta miqe tana fatan Ya haiqewa Falaq sbd itace AZIZ LIMBA zaifi haukacewa akanta,

Ita kuwa Mama ajiyan zuciya ta sauke tana jin kome zaiwa Jannah tinda daman aurenta zaiyi da saukobatareda tasan menene a zuciyar Nicky akan Falaq ba,
Hakama kodai baiwa kowa komaiba yayi attempting ta yanda AZIZ zai Koresu dan itadai fatarta kawai a koresun koma menene laifin.

Wannan ne kadai zai faru a gidan AZIZ ya tsani Jannah ya Koresu su huta duka da wannan masifar da basusan ranar qarewanta ba.

*****Karfe 7 suka gama ayyukansu suka bar kitchen din,

Zazzbi Jannah taji tanaji me karfi sbd koin jikinta dake zafi dan haka bata iya zama cikin su Maheer ba daki ta wuce ta sakarwa jikinta ruwa sbd jin abin na neman fin karfinta.

Ummah ma wani irin zafi jikinta yayi Wanda ya saka Dad tinanin batada lafiya ga zufa tanata yi sai fita yake mata.
#MAMUH
#LIMZAD
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 30

*_SHOP WITH ME BY RANO_*
08030811300
https://chat.whatsapp.com/IexiuY21PP75lt4yoJtNsK
Kina neman in da zaki samun kayan yara classy kaya na yan gayu at a very affordable price? Ko kina son fara kasuwancin kayan yara amma baki da jarin da zaki saro kayan? Nesa ta zo kusa, kiyi joining community din nan muna saka kaya masu kyau available da inganci a farashi me sauki da zaki dauka ki tallata har ki samu naki kema.
Burinmu shine kowacce mace ta samu sanaar da zata dogara da kanta.

*****************
Yanayin Ummah da kaman zazzabita ke qara qarfi da Jannah daman da bata samu fitowa ba ya saka kowa ya watse suka shige da wuri daman kowa a gajiye yake.

Fatma ko data shigo daki karfe 9 ta dan wuce Amma har lokacin Jannah bata saka kaya ba duk sanyin dakin na ac zufa takeyi tana zaune ta qanqame jikinta.

Qarasowa Fatma tayi tana kallanta cikin mamaki tace

"Jannah kina lafiya kuwa?

Kasa dago jajayen idanuwanta da suka shige ciki sosai tayi ta kalli Fatman ta dauke kafafunta daga qasa tana hawowa gadonta dasu ta girgiza kai ahankali alaman batada lafiya batareda ta iya bude baki ba.

Sake kallanta Fatma tayi da kyau taga kwata kwata bata cikin yanayi me kyau hakama zufanta sai qaruwa yakeyi.

Abin fita Fatma ta juya ta dauko tareda dawowa ta zauna kusa da ita tafara mata fita tana saka abu me kyau tana share mata zufan dayake ya sake jiqata.

Bude ido Jannah tayi tareda kallan Fatma idanuwanta na cikowa da hawaye da sanyin murya

tace

"Fatma kaman jinina Yana konewa nakeji,
Kaman zan mutu nakeji?
Bansan meya sameni ba hadda marana Yana ciwo...."  Hawayen idonta ne suka gangaro tana rintse idanuwan tana kwantawa jikin na dan fara rawa.

Damuwa da tsoro Fatma ta dan shiga ta kalleta tace

"Jannah ko naje na fadawa Su Dad ko Maheer ne ko zaa kaiki asibiti ne?

Girgiza kai tayi tana tashi zaune ta ziro kafafunta qasa tana saukowa daga gadon ta nufi toilet ta sake saukarwa kanta ruwa sbd anan ne take samun dan sassauci.

Bakin toilet din Fatma ta tsaya har Jannah din ta fito suka sake komawa bakin gado zuwa lokacin Jannah ta fara maye ta jiqo har dogon gashinta dayake a kunce Wanda a ranar Fatma ta wanke mata shi zasuyi kitso bata samu anyi ba sai gobe Fatman tai mata.

Gabaki daya jikinta ta jiqasa ta fito tana tafiya ahankali idanuwanta sunyi wani laushi sosai cikin mayen data fara tace

"Fatma ruwa"

Ruwa Fatma ta tashi da sauri ta dauko mata ta bude mata ta bata a baki tana goge mata ruwan dake gangarowa daga gashinta suna sauka jikinta.

Tin lamarin na kadan kadan har dare ya qara tafiya Fatma na fama da ita zuwa lokacin gabaki daya hankalinta ya gama tashi ta shiga tsoro sosai kada wani abin ya faru kafin safe ta rasa me zata fadawa su Dad.

A daidai wannan lokacin Dad na can na yana fama da Ummah itama a cikin irin wannan halin sbd nata daya hada da rashin lafiyan kwakwalwa sai itama lamarin yayi nauyi sosai.

Yanayin yanda take zufa da dafe mararta tana cewa "Dad ciwo sosai anan" ya saka yafara tinanin mara take nufi,

To meya hadata da ciwon mara shine ya fara tinani kafin ya sake kaita toilet ya zare mata doguwar rigarta yabarta daga ita sai farar vest qal dake jikinta me dan tsayi ya kunna mata shower Yana goge mata ruwan dake sauka kan fuskanta sbd kada ta shaqa ruwa.

Daga shi har ita duka sun jiqe sbd ta kasa tsayawa murkusus takeyi sosai tana cukuikuyesa karshe ma kuka ta saka masa wanda ya rasa ya zaiyi sbd damuwa da tsananin tausayinta ya rungumeta Yana dawo da ita daki aka cire jikakkun kayanta ya saka mata wasu kayan marasa

nauyi na bacci sedai gabaki daya ta qarasa rikice masa dan haka ya kwantar da ita jikinsa Yana mata addua yanajin tana cakudasa cikin wani irin mayen dayake rufeta koinanta.

Rintse idanuwansa yayi ahankali yanajin wani irin yanayin datake kokarin tayar masa wanda ya dade da dannewa riqewa sbd tinda ya aureta bai taba mata komaiba sbd Yana fatan ta samu cikakkiyar lafiya ta amshesa a matsayin mijinta a hankalinta Amma ayau kaman hakan bazai yiyuwaba sbd ita kanta kaman ciwon dayake neman illata kenan a cikin Daren.

****Fatma ganin masifar dake neman fin karfinta cikin karfin hali ta kama Jannah din ta saka mata qaramar rigar shan iska da hijab suka fito tana dan riqe da ita sbd su samu iskan waje ya daketa ko zata dena wannan zufan datake tayi.

Fitowa sukai lokacin karfe goma sha daya saura dan haka sunsan kowa ya shige.

Suna fitowa iska me dan karfi ya fara buga Jannah din wadda tafara jero ajiyan zuciya tana rufe idanuwanta.

Fili suka fita sosai inda iskan yafi kadawa Fatma na riqe da Jannah din har lokacin tana mata sannu.

Hasken mota ne ya sako kai harabar gate na biyun gidan wanda garba ne da bai shigeba sbd Sanin me gidan be dawoba yaje ya bude musu gate motar black Royce Royce ta sako kai cikeda wani irin rashin kukan dayake bayyanarda ba kudin qananun masu kudi ke siyanta ba.

Garba na rufe gate din ya juya ya nufi hanyar dakinsu ya shige batareda ya hango su Jannah din ba.

Fatma dake cikin tsananin damuwa ita kanta bata wani damu da waye ya dawo ba bare Jannah da batama ji ko ganin komai sbd ita kadai tasan masifa da balain take ciki.

Kashe motar Sayd yayi tareda dan juyowa ya kalli AZIZ Wanda ayau baida niyar kwana baiga Jannah dinba dan haka m wayar Falaq yake kokarin kira dan aikata neman Jannah din
Cikin sanyi da mamaki sayd Yana maida kallansa kansu Fatma yace

"Kaman 4&4 ce acan tareda dayan me aikin"

Dakatawa AZIZ din yayi daga Kiran dayake kokarin sakawa tareda dagowa ahankali ya sauke idanuwansa akan inda Sayd din ya fada.

Ba haske sosai a gurin Amma kallo daya yayiwa gurin ya ganta tsaye a jikin Fatman.

Kashe wayarsa yayi gabaki daya tareda ziro kafafunsa waje daga kofar da sayd harya fito ya

bude masa.

Kai tsaye inda take ya nufa Yana dago hannunsa ya kalli time ya maida kallansa akanta Yana qarasowa.

Fatma da bata lura dashi ba sai dataji wani fitinanniyar qamshi na dosota ta juya tagansa yana qarasowa bata fa fuskansa ba saida ya iso gap dasu fuskansa ya bayyanar mata,

Mugun firgita tayi da ganinsa gabanta na mugun faduwa dan haka a rikice tayi baya tana sauke kanta qasa tana dabarcewa tareda manta halinda Jannah ke ciki a jikinta.

Janyewanta ya saka Jannah da bata iya tsayuwa se a jikinta din zamewa zata zube qasa.

Hannu daya ya saka ya tarota batareda ya bari ta kai qasa ba Yana kallan fuskanta da idanuwanta suke rufe tana sauke numfashi me tsananin rashin karfi.

A jikinsa ta zube Yana sake riqeta jikin nasa da kyau ya dauke idanuwansa akan fuskanta dake bayyanarda ba lafiya take ba kwata kwata ya kalli fatma wadda ta sake qasa da kanta sosai cikeda girmamawa.

Bude baki yayi a natse da kamewa yace

"Me yake faruwa?

Cikin kama kai Fatman ta bude baki tace

"Batada lafiya tin dazu kuma ta hana na fadawa su Dad"

Sayd daya iso lokacin kallo daya yayiwa Jannah din daga jikin AZIZ din ya dauke idanuwansa Yana dawo dasu kan fatma yace

"Tsawon awa nawa ne?

Shiru tayi sbd bazata iya Tina ko awa nawa bane.

Magana AZIZ ya bude baki zeyi Jannah ta dago kanta tareda sama da kanta zuwa cikin wuyansa ta shago qamshinsa taja cikin hancinta tareda bude idanuwanta da sukai jajir tana kallan bakinsa daya bude zeyi magana take taji wani irin maitarsu na cikata ta dago hannunta ahankali ta Dora akansu tai musu wata irin shafar data sakasa mutuwar tsaye yana kallanta da tsananin mamaki.

Sayd saurin sauke kansa yayi Yana dan ja da baya batareda ya dago ba.

Fatma ma rikicewa ta qarasa yi ta juya batareda ta Sani ba ta ringa jefa kafarta duk inda ta samu tabar gurin zuwa dakinsu.

Riqeta yayi da kyau ganin tana kokarin zubewa qasa ya kalleta da kyau yaga tana sake jiqewa da zufa.

Fuskanta ya Shafa ahankali Yana goge mata zufan fuskanta da handkerchief dinsa daya ciro daga aljihu ya bude baki cikin sauti mara hayaniya da tsananin kulawa yace

"Menene kikeji Yana damunki?

Girgiza kai tayi batareda tasan tayi ba kafin ta bude idanuwanta ta saukesu akan lips dinsa dake motsawa suna maganar da batajin komai jinta ya dauke..

Gangaro da idanuwanta tayi wuyansa dayake motsi ahankali Shima ta sake dago hannu ahankali ta shafi wuyansa tana yi sama ta sake shafan lips dinsa tareda hadiye wasu yawun da suka wuce maqoshinta ahankali tanajin taste din bakinsa a nata bakin...

Ganin tsayuwar ta gagara ya dauketa gabaki dayanta ya juya ya bar gurin da ita.

Sayd na ganin hakan ya wuce gaba da sauri ya bude masa kofar da zai wuce kai tsaye Yana isowa ya shige da ita tana sake cusa kanta cikin wuyansa tana janyo qamshinsa dake qara tsananta halin datake ciki.

Babu kowa a palon qasan sai fiddausi data sauko daukan ruwan daya qare a  palon sama zata kai tana fitowa kitchen Yana sako kai palon da Jannah din dan haka itama da sauri ta dakata tareda komawa baya kitchen din tana sauke kai qasa.

Samansa ya wuce shikuma Sayd ya tsaya ya rufe koina kafin ya wuce nasa dakin.

Fiddausi data tabbatarda sun shige ta fito itama ta haye nasu saman tana isa a palo data bar Mama da Nicky suna fira cikin tsananin nishadi ta kalla cikeda mamakin Mama da bata kai wannan lokacin batai nisa a bacci ba.

Cikin mamaki tace

"Mama haryanxu biki bacci ba lokacin baccinki yanzu ya sauya lafiya ta qara samuwa yanda mukeso"

Duk da Maman na fushi da fiddausin har lokacin Amma tinda sun sama sakewansu kuma tana cikin farin ciki dan haka Murmushi tayi tana cewa

"Eh yau dai kam baccin ya tafi sai zuwa anjima kila kokuma dan nay baccin rana ne"

Itama fiddausin cikin murmushi da nata farin cikin tace

"Nima dai yau banajin baccin Nan bara na kai ruwan fridge Nazo na taya Mama da 'yarta fira mu raya Daren kila alkhairi ne a cikinsa"

Nicky da takejin kaman tayita ihun farin ciki cewa tayi

"Kwarai wannan Daren na alkhairi ne"

Mama dai murmushi kawai takeyi tana hadiye dadinta ita kadai.

Fiddausi na ajiye ruwan ta dawo ta zauna a cikinsu suka hau fira duk da hankalinsu na kan madam Sisi da suke jiran ihunta sbd Nicky ta tabbatar mata kada tayi bacci tayi gadin bangaren su Jannah tana ganin Ammar ko alaman namiji tayita kurma ihun da kowa seya fito.
#MAMUH
#BEST LOVE
#TOO HOT
#ROMANCE
#JANNAH ZAD LIMBA

07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 31

*_SHOP WITH ME BY RANO_*
08030811300
https://chat.whatsapp.com/IexiuY21PP75lt4yoJtNsK
Kina neman in da zaki samun kayan yara classy kaya na yan gayu at a very affordable price? Ko kina son fara kasuwancin kayan yara amma baki da jarin da zaki saro kayan? Nesa ta zo kusa, kiyi joining community din nan muna saka kaya masu kyau available da inganci a farashi me sauki da zaki dauka ki tallata har ki samu naki kema.
Burinmu shine kowacce mace ta samu sanaar da zata dogara da kanta.

************
Dukkaninsu bacci ne yake zuwar musu me karfi Amma zuciyoyinsu sun kasa yadda da baccin dan haka suka qara nacewa Daren,

Fiddausi data gaji bazata iya ba ta miqe ta shige daki tabarsu Anan wanda ba jimawa dukkaninsu suma baccin ya daukesu a palon.

AZIZ kuwa Yana isa sama ajiyeta yayi a tsakiyar palonsa Yana kokarin zare mata hijab dinta sbd ya qara mata AC kafin ya samu daman Kiran Sayd ya kira mata likita Amma Sam ta kasa tsayawa,

Bayason ciro mata hijab din ta qasa yazo wuyanta ya bata matsalar nade mata fuska Tasha wuya bayan wadda yaga tana Sha zuciyarsa bazata dauka ba dan haka daga wuyanta ya yaga hijab din yana zame mata shi qasa yana sake kamo fuskanta ya amabaci sunanta cikin kulawa Amma bata amsaba sai binsa takeyi da wani mayen kallo da idanuwanta dake kashesa...

Gashinta dayake a jiqe ya kalla kafin ya gangaro da idanuwansa wuyanta yaga ruwa kaman na gashin kaman zufa ya dago idanuwan ya kalli fuskanta itama shi take kalla har lokacin tana sake shiga yanayinsa..

Daukanta ya sake yi ahankali ya isa kujera da ita zaunar yaje ya dauko qaramin towel me kyau ya dawo,

Rankwafowa yayi gabanta ahankali cikin nutsuwa Yana sake ambatar sunanta da wani natsatsen sauti yana kai towel din wuyanta ya shafo tareda kai hannunsa daya Yana janye mata gashin fuskanta...

Numfashinsa me dumin gaske ne ya sauka a fuskanta da wuyanta daya matso yana goge mata wuyan ta rufe ido ahankali tana jin gashin jikinta gabaki daya suna miqewa taja wani kasalallen numfashi...

Saukan lallausan tafin hannunsa akan fatar wuyanta yana gogawa ya sakata bude ido akansa tareda Jan wani sabon numfashin daya sakasa kallanta Yana karantar yanayinta Wanda kusan idan yana karanta daidai tana cikin tsananin desire ne Wanda yasan bata hankalinta dan idan tana ciki bazata taba nemansa ba sbd fushinta akansa,

Ina ta hadu da koma menene?
Waye ya bata? Sbd yasan har abada bazata taba shan koma menene a Karan kanta ba?

Kukan data fasa ahankali ne ya sakasa  kallanta Yana bude baki zeyi magana ta rigasa cikin kuka da cewa

"I hate you AZIZ LIMBA"  da qarasa maganar ta kamo gaban rigarsa tareda fizgosa da karfi ta kalli lips dinsa da suke kaman fresh ta kai bakinta akansu tana hadesu da nata tareda bude bakinta tana jefa harshenta a bakinsa tana masa wani irin lafiyayyan shan daya saka towel din hannunsa faduwa Yana jin duniyarsa data wargaje tana haduwa guri daya.

Kissing din data kewa bakinsa tana jin dukkanin zafin jikinta na ragewa Yana sauka ya saka

kanta sake juyewa ta saka hannuwanta biyu ta zagayo wuyansa tana lumshe idanuwanta qamshinsa kawai yana sake kashe wutar dake ci a jikinta.

"Sorry 4&4" ya furta a hankali bakinsu na hade kafin ya saka hannuwansa biyu ya kamo qaramin qugunta yayo sama da ita Yana fara tsotsan bakinta cikin wata irin nutsuwa da tsananin sonta dayake cin jini da zuciyarsa kowace daqiqa.

Kan ctable ya zauna tareda bude kafufunta ya zaunar da ita akan kafafunsa suna fuskantar juna ya bude jajayen idanuwansa Yana bin fuskanta zuwa wuyanta da kallo Yana jin kaman ya hadiyeta da dukkaninta sbd abinda yake ji akanta.

Itama shi takewa wani irin kallo a cikin mayen dayake sake juyata....

Rigar dake jikinta mara nauyi ya tattaro ahankali Yana Shafa lafiyayyun cinyoyinta bakinsa yakai gefen kunnenta ya sakar mata numfashi me tareda zira harshensa ahankali ya laso fatar hannunsa na isa kan mararta da yayiwa wata irin shafa da tafin hannunsa taja numfashi me karfin gaske tana zagayo wuyansa da hannunta daya dayan kuma tana bin hannunsa cikin rigar ta dora akan nasa hannun tana jin kaman zata zare.

Cibiyarta ya Shafa ahankali Yana sake cusa kansa cikin wuyanta Yana sakar mata kiss masu sanyi da numfashin dayake sake saka jikinta daukan zafi.

Sama yafara yi da hannun Yana Dora bakinsa akan bakinta Yana tsotsa lips dinta da sukai jajir....

Saukan hannunsa a samanta ya saka su biyun numfashinsu daukewa a lokaci daya Yana sake matseta da karfi jikinsa..

Gashinta ya kama yayi baya dashi kanta na baya ya saka kansa cikin rigarta gabaki daya yana hadesu guri daya..

Bude idanuwanta ta basa ganin komai da komai bayan shi kadai da zuciyarta takewa so daya babu wani bayansa ta zagayosa da hannuwata tana son bude baki tayi magana Amma bata iyawa sbd abinda yake faruwa a cikin rigarta da kansa yake ciki...

Numfashin dayake fitowa daqyar take saki tana neman rasa kanta gabaki daya tana sake rungume Kansa cikin tsananin shauki da son daya taso mata gabaki daya a cikin yanayin.

Kansa na ciki ya saka hannu ya zare musu rigar wadda ta barta babu komai a jikinta sai black panties...

Hannuwanta ta saka ahankali gaban tsadaddiyar rigar dake jikinsa ta budeta gabaki daya lokaci daya botiran rigar suka zube qasa ya dago Yana mata wani mayen kallon dake bayyanarda

wannan moments sune best moments na rayuwarsa sbd idanuwansa dake nuni da hakan tareda mamakin 4&4 dinsa dayake sake jinjina karfin abinda yake aiki akanta.

Wurgi tayi da rigar jikinsa shi kuma ya saka hannu ya mannota kirjinsa da nasa suka hadu ya lumshe ido Yana Jan wani fitinanniyar numfashi me karfin gaske ya budesu akanta ya bude baki daqyar yace

"4&4 banason da safe ki tsani kanki akan abinda yake faru.....

Bai qarasa ba ta saka bakinsa cikin nata tana sake mannuwa dashi.....

Miqewa yayi da ita a jikinsa qafafunta na zagaye dashi ya nufi bedroom dinsa da ita Yana zuqo yawun bakinta da ko iya su darajarsu tafi masa duk abinda ya mallaka yana.

A lafiyayyan gadonsa ya jefata ahankali Yana zare doguwar Sweatpnt din dake jikinsa Yana binta da wani mayen kallon dake sake juyar da kansa.

Bakinsa ya dora akan Mararta ya sakar mata wani irin zazzafan kiss tareda saka harshensa ya lashi cibiyarta ta qanqame pillow da karfi tana rasa numfashinta na Yan daqiqu...

Asalin lafiyayyar fatarta me laushi da tsafta ya saka harshensa Yana lasa Mararta zuwa cibiyarta ya qarasowa tsakiyar kirjinta inda da harshensa da numfashinsa a tare suka sauka ta bude baki zatai wani irin numfashin cetan Rai ya dago kanta Yana rufe bakinta da nasa yana hannunsa na bin kirjinta zuwa bayanta da wata irin shafar datake sake rabata da numfashinta Amma ya hana hakan sbd bakinsa dayake bata wata irin tsotsan da taste din bakinsu ya zama daya...

Yanayinsa fara fin karfinsa yayi yafara loosing control na kansa sbd yanda yake yake tsotsanta Yana bata zafafan romance Musamman kirjinta da sukai jajir dan haka zai iya kasa riqe kansa yayi abinda zata tsanesa idan ta dawo hankalinta shi kuma zuciyarsa da rayuwarsa bazasu iya daukan tsanar da zatai masa ba...

Juyar da ita ya ta kifu a gadon ya kwanta bayanta hannunsa daya na zagaye da kirjinta daya dake tafin hannunsa hannunsa daya kuma Yafara Shafa bayanta ahankali Yana sakar mata kiss me sanyi a bayan wuya da gefen fuskan Yana sakar mata numfashi me sanyi a cikin kunnenta idanuwansa a lumshe yana jin dumin jikinta na shiga jikinsa ahankali Yana sauka.

Numfashi suke saukewa ahankali dukkaninsu itama idanuwanta a lumshe tana samun relief da saukar abinda take ji yana quna a jininta,

Jikinsa dayake rawa na yanayinsa dayake cinsa ya sakasa sake rintse idanuwansa Yana jin wani irin yanayi a zuciyarsa da bazai iya rayuwa ba duk yanda zai samu gwarin gwiwa idan ya

rasa 4&4,

Rashin Ummansa Ummitah ce ta zama qwarin gwiwa da fitilan data haska rayuwarsa harya cigaba da rayuwa,

Bayan rasa Ummitah Falaq ce ta zama jagorar data kawo rayuwarsa a yanzu,

Bazai iya rasa Jannah Zad ba sbd a duniya babu abinda zai iya hanasa fading idan babuta a rayuwarsa,

Lumshe idanuwansa yayi da sukai jajir ruwa masu tsananin dumin dake cikinsu suka gangaro suka sauka akan bayan wuyanta tareda gangarowa ahankali suka diga gaban idonta data bude jin saukan dumin ruwan..

Ahankali itama idanuwanta suka ciko da hawayen abinda take ji a zuciyarta akansa,

Gangarowa sukai gefen idonta suka sauka tanajin rawan da jikinsa keyi tana qaruwa sosai ahankali ahankali na tinanin dayake cin kwakwalwansa da zuciyarsa....

Tsananta yanayinsa keyi har Yana jijjigata ita da jikinsu yake hade.

Zamewa yayi Yana qanqame jikinsa ya sauka gadon Yana sake jijjiga ya nufi toilet idanuwansa na rufewa.

Yana shiga tin bai qarasa ba ya zube qasa yana riqe kirjinsa Yana kokarin miqewa ya isa ga shower...

Gudu hawayenta suka tsananta yi tana jin zuciyarta na bude dukkanin wani tsohon ciwo da raunin zuciyarta...

Bata gama dawowa daidai ba sbd abinda yake jikinta bai gama sakintaba
Kasawa tayi dan haka ta sauko gadon itama da qyar ta nufi toilet din tana shiga Yana durqushe cikin mummunan halinda ya kasata qarasawa da sauri ta zube gabansa tareda rungumesa gabaki dayansa a jikinta tana ambatar sunansa ahankali wanda sautinsa ma ya banbanta da yanda a yanzu take kiransa sbd wani irin tsananin so da kewan datake cikin wannan.

Hannu ta miqa ahankali ta kunna musu ruwan Yana sauka akansu ta kamo fuskansa da tafukan hannuwanta biyu ta kallesa cikeda yanayin da batasan yaya zatai da zuciyartaba ta bude baki tace

"AZIZ LIMBA I hate....."

"But I love you JANNAH ZAD." Ya fada daqyar cikin wani irin mummunan yanayi Yana katseta batareda takai karshen maganarta ba da zuciyarsa bazata iya dauka ba.

Rintse idanuwanta tayi tana kokarin zamewa ya riqeta tareda hanata zamewa ya kalli cikin tsakiyar idanuwanta yana saka bakinsa akan nata yana shigar harshensa ciki.

Qanqamesa tayi tana karbansa ahakan....

Fatarta dake bawa tasa nutsuwa ya sake janyowa cikin ruwan Yana cigaba da kissing ruwa na sauka akan fatarta dake saks santsi a tasa fatar Musamman yanda suke cakuda babu me riga a jikinsa.

A jikinta ya samu nutsuwarsa ta dawo zuwa lokacin zazzabi me karfi ya rufeta sbd maganin dayake kokarin sakinta da kuma ruwan data shiga sosai tsakanin fara ciwon.

Da kansa ya dauro mata towel suka fito ya rage ac din dakin tareda dauko rigarsa me dan kauri ya saka mata tareda bata ruwa mara sanyi Tasha ya kwantar da ita jikinta na rawa sosai sbd take jikin yayi karfi.

Kwantawa yayi gefenta ya rufesu tareda shigar da ita jikinsa sbd ta sake samun dumin datake buqata.

Shi kansa Kansa a nauyaye yake dan haka ba bata lokaci baccin ya daukesa.

Itace tafara farkawa da asuba taji sauki ba laifi dan haka ta miqe.

Tashi yayi shima Yana taba jikinta yaji da sauki ya kalleta zaiyi magana ta katsesa cikin rashin sakewa da rashin walwala tace

"Pls don't"

Fasa maganar yayi ya kalli toilet da ido ya nuna mata.

Saukowa tayi da dan sauri ma tayo alwala ta fito
Shima alwalan yayo sukai sallah.

Suna gamawa ta miqe ta nufi kofa da sauri gabanta na faduwan kada tsautsayi yasa wani yasan a inda ta kwana.

Hijabinta ta dauka a yagensa ta saka ta fito AZIZ din na biyeda ita tareda riqo hannunta a natse yace

"Ki nutsu baki gama warware ba and I need to talk to you akan abinda ya sameki"

Bata amsa ba take tafiya tana son qwace hannunta Amma Sam yaqi saki har suka isa kofar bangarensu bai damu da komai ba ya shigo daidai lokacinda Madam Sisi ta gama baccinta ta Tina da aikinta aka sakata Wanda bacci ya saceta sai yanzu.

Inuwar namiji da mace ta gani a daidai kofarsu Jannah din wanda ya sakata bude ido da karfi tana sake tabbatar da mace da namiji ne take gani kuma hannuwansu a riqe....

Fili ta fito yanda kowa zeji ta bude baki duk iya karfinta ta fasa ihun a kawo musu dauki kwarto.

Wata mummunan faduwa gaban Jannah yayi ta juya a rikice ta kalli kofar dakin Dad datasu Maheer da ake kokarin budewa cikin saurin jin ihun.

Kafin AZIZ din yayi kowane irin motsi ta kama hannunsa da karfi ta bude dakinsu ta turasa tareda shigewa tana rufewa daga ciki.

Tana rufewa Ammar da Maheer na fitowa cikin tsananin tashin hankali da makamansu a hannu.

Ammar dakin su Jannah din ya nufa Yana tare kofa,

Dad ma a rikicen ya fito yana saka jallabiya,

Su Mama ma cikin bacci suka firgita tareda miqewa tsaye suna rige rigen fitowa itada Nicky suna taya Sisin ihu.

Sayd ma dauke da pistol dinsa ya fito yana busawa securities whistle take gidan kowa ya miqe tsaye cikin tashin hankali da tsananin duhun asubar.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 32

*_SHOP WITH ME BY RANO_*
08030811300
Kina neman in da zaki samun kayan yara classy kaya na yan gayu at a very affordable price? Ko kina son fara kasuwancin kayan yara amma baki da jarin da zaki saro kayan? Nesa ta zo kusa, kiyi joining community din nan muna saka kaya masu kyau available da inganci a farashi me sauki da zaki dauka ki tallata har ki samu naki kema.
Burinmu shine kowacce mace ta samu sanaar da zata dogara da kanta.

*************
Ihun Nicky da Mama ne ya sake karade gidan suna nufo scene din,

Fiddausi ma da duk basu kai ga tashi sallar asuban ba cikin bacci taji ihun kwarton da neman agaji ta bude ido tana dirowa gado bata tsaya saka komai akan kayan baccin jikinta ba ta fito da gudu a firgice gabanta na tsananin faduwa da tsoro.

Dakin Falaq take kokarin nufa ta dubota hankalinta tashe saiga Falaq din itama ta fito a tsananin tsoroce jikinta na rawa idanuwanta na qanqancewa tana ganin fiddausin ta iso gurinta da gudu tana cewa

"Fi waye kwarto?
Meye hakan??

Fiddausi data samu ganin Falaq din a gabanta kalau numfashi ta ajiye ta fada maye ake nufi da hakan,

Da sauri falaq ta juya jikinta na tsananta rawa ta nufi stairs da tsananin gudu kaman zuciyarta zata fado sbd jin bangaren masu aiki ihun ke tsananta Wanda tasan Jannah dinta na can zuciyarta bama zata kwatanta wani abu ya taba Jannah ba,

Biyota fiddausi tayi da tsananin gudun kada taje ta hadu da kwarton tinda kila neman gudu yake daga gidan..

Su Mama na isa idanuwansu sun rufe basa gani sosai hakama bacci bai gama sakinsu ba gaba daya dan a cikin bacci kawai sukaji ihun take suka karba suna rige rigen fitowan dayake da abin suka kwana a Rai,

Duhun asubar da rashin hasken gurin sosai y saka basu gane waye da waye a tsaye a gurin ba dan haka Nicky ta fara ihun cewa

"Ku balla dakin ku fito da Ammar din,
A kira AZIZ,
Ina securities? Wayyo kwarto"

Madam Sisi kuwa har gurin hanyar bangaren AZIZ ta isa ta ringa ihun kwarton tana neman agaji.

Securities da Sayd dayake Daga pistol din hannunsa baya cikin flowers din gidan suka nufa d manyan haske Sayd na cewa

"Kuna ganinsa ko waye ku harbe kafarsa duka biyun a take Umarni ne"

Maheer da Garba dake dauke da manyan sandunan gora suma bayan dakunansu suka zagaya Dad na zagayawa bayan dakin su Jan da wuqar daya fiddo.

Ammar kuwa dakinsu Jannah ya tsare dan bada kariya dan yafison Yana ganin duk abinda zai shiga dakin ya sare wuyansa da karfen hannunsa,

Mama ganin gida ya rikice har lokacin Nicky da madam Sisi ihu sukeyi ba AZIZ bai fitoba ta nufi bangarensa da gudu tana sake goge idanuwanta da basu qarasa washewa ta riga kwala masa kira.

Daga waje ma sauran securities din sun zagaye gidan an basu umarnin duk wanda suke gani su harbesa a spot din.

Gabaki daya hankalin maqotansu sauran mansions da gidajen manya dake gurin tashi hankalinsu yayi  sbd ihun d tashin hankalin yayi yawa hakama sai harba bindiga akeyi sama wadda ta saka securities na anguwa gabaki daya suma miqewa tsaye aka hau zagaye unguwa da shirin harbe duk Wanda aka gani shine kwarton.

Fatma da balain da masifar ya sakata tashi a firgice cikin baccin da bai dauketaba sbd gadin jiran dawowan Jannah sai asubar me nauyi ya dauketa.

Tana bude idanuwanta a rikice taga mutane tsaye tsakiyar dakin Jannah na qanqamesa da karfi idanuwanta cikeda hawaye tana rokonsa kada ya fita a lokacin shikuwa Kansa Yama kasa daukan uban waye yake ihun kwarto a cikin gidansa sannan ita ta sakasa daki ta boye?

Fatma datake a rikice da ihun su Madam Sisi kurma sabon ihun tayi sbd da duhu a dakin ba haske tana miqewa da tsananin gudun gaske itama ba Kayan arziki a jikinta ta banka kofa da gudun gaske ta fito tana taya su Nicky ihun.

Rintse idanuwansa d sukai ja sbd tsananin bacin rai yayi zai yi magana jannah tayi saurin saka hannunta dake rawa bakinsa tana rungumesa cikeda tsoro da kunyar da zata iya kasheta idan ya fita.

Nicky na ganin tsananin tashin hankali da firgicin da Fatma ke ciki bata tsaya wata wata ba ta nufi dakin ta fada tana tsananta ihunta sbd ta tabbata Ammar da Jannah suna ciki.

Tana sako kai cikin duhun dakin tana ihun AZIZ da yagama kai maqura a bacin ransa hannu ya daga ya zabga mata wani mahaukacin marin daya sakata zubewa baya tana fadowa Madam Sisi data biyota suka zube qasa take jikin madam Sisi ya dauki muguwar rawa cikin tsananin mugun tsoro ta ture Nicky da karfin gaske tana miqewa ta bar gurin da gudu tana cewa

"Wlh yana dakin,

Gashinan a ciki"

Mama n jiyo hakan ta dawo da gudu duk a rikice,
Su Maheer ma dasu Sayd zagayowa da gudu dukansu sukai gabaki daya gidan suka taru a kofar dakin,

Zaadens da sukasan zinariyarsu n ciki take suka qarasa haukacewa suna tinkarar dakin da karfin gaske.

Falaq dataji Jannah na ciki hakama kwarton kasa riqe kanta tayi da gudun da babu wanda ya ankara ta wuce kowa ta isa kofar dakin jikinta n Tsananin rawa ta tura kofar dakin daidai Jannah zata rufe dakin d key.

Da karfin gaske Falaq ta fada jikin Jannah din tana qanqameta jikinta na rawa har lokacin ta fasa kuka tana sake kankameta kaman zata shige jikinta.

Gari ya fara haske dan haka Sayd yayi saurin cewa kowa ya dakata da makaminsa sbd Falaq data tare kofar..

Kuka takeyi sosai tana sake qanqame Jannah,

Jannah dake rikice cikin tsananin tashin hankali kasa motsawa tayi tana kokarin janye Falaq din Falaq ta bude idanuwanta ahankali kaman a mafarki idonta ya sauka akan Daddynta dayake tsaye dukkanin bacin rai da fushinsa a fili amma ya kasa take rokon Jannah din ya fito yaci uban duk wani mahaukacin dayake gidansa.

Da tsananin mamaki me karfi ta saki Jannah ahankali tana kallansa kafin ta dawo da kallanta kan Jannah Wadda kunya ta sakata qasa da kai.

Juyowa Falaq tayi da sauri taga yanda kowa yayi cirko cirko tsuru tsuru suna jiran ta fadi abinda ta gani sbd sun tabbatarda duk abinda yake bayan Jannah cikin dakin ta gani.

Cikin ihu Fatma tace wlh naga mutum a cikin dakinmu,

Madam Sisi da tin dazu take zuba rantsuwar taga kwartaye da idonta karbe zancen tayi tana maimaitawa.

Nicky da tini jinta ya dauke sbd Marin datasha hakama ganinta rawa yake a hakan ta saka aka kawo mata wayarta ta kunna recording dn kofar dakin sbd tanason nunawa AZIZ lokacinda aka kamasu suna fitowa dakin.

Juyowa Falaq tayi ta sake tare kofar ita kuma Jannah ta sake kama hannunsa ta jasa bayan kofa tana sake riqe hannunsa cikin nata idanuwanta duk sunyi ja kuka takeson yi sbd abinda

take ji na wannan mugun yanayin da suka samu kansu.

Falaq bude hannuwanta tayi ta sake tare kofar ta bude baki tana kallan Sayd tace

"Ba kowa a ciki Jan ce kadai"

Mama da duk ta haukace tace

"To ta fito mana me takeyi a dakin kowa ya fito dan wanke Kansa"

Sayd Falaq ta kafawa ido Wanda yake kokarin fahimtar me take son fda masa tace

"Papa ina Daddyna? Sai yazo zan matsa jikin kofar Nan"

Sayd na jin hakan ya kalli kofar dakin da sauri Ya juya ya kalli fiddausi wadda itama take ta shiga shock ta kallesa tana soke kai.

A rikice Sayd din ya fito yana cewa securities su koma bakin aikinsu,

Kallan kowa yayi zaiyi magana Ammar cikin tsananin zafi ya katsesa da cewa

"Karma hauka ta debeka kace mubar gurin Nan sbd wlh duk abinda yake dakin Matata saina shiga na dubosa idanma mutum ne ya Sani yau kwanansa ya qare,
Waye ya isa ya shigarmun gon...

Kaman saukan tsawar aradu suka ji wani mahaukacin ihun tsawarsa yana bayyana gabansu idanuwansa jajir kaman zasu kama da wuta ya bude baki gabaki daya gidan Yana daukan sautinsa yace

"Securities,ku bude motarku duk Wanda yayi ihun kwarto da duk Wanda ya dauki makami a cikin gidana ko waye da waye ku kwashesu gabaki daya ku kai office ku rufemun"

Jannah dake bayan kofa silalewa qasa tayi tana cusa kanta cikin kafafunta kuka me karfin gaske na zuwar mata.

Mama kuwa jiri ne ya debeta taji kaman rabin jikinta na neman shenyewa idanuwanta na kasa gasgata AZIZ da kansa a dakin masu aiki.

Nicky wayar hannunta ce ta kubuce daga hannunta ta fadi qasa hannuwanta na kakkarwa sbd kasa gasgata abinda idanuwanta suka ganar mata AZIZ LIMBA dinta bangaren masu aiki kuma a cikin daki.

Su Dad kuwa tsananin tashin hankali da shock din da suka shiga ya saka su kasa motsawa Banda Maheer daya Yar da makamin hannunsa Yana isa dakin da sauri ya shiga dan dubo Jannah.

Yana shiga ya isa gurinta da sauri Yana dagota ta rungumesa tana fasa kuka me karfi tana cewa

"Maheer babu abinda yazo yi ba girina yazo ba babu ruwana dashi ba abinda yake tsakanina dashi"

Ynada take maganar tana kuka sosai ya saka jikinsa sanyi hakama Dad da Ammar Wanda yayi mutuwar tsaye sanyi sukaji jikinsu yayi sbd sun tabbatarda Jannah bazata taba komawa AZIZ ba tagama dashi har abada hakama bazata taba musu karya akansaba.

Securities da sukafi kowa hauka akan umarnin uban gidansu da ayau suka tabbatarda a zafafe yake tini suka taho da mota doguwa a rife koina aka bude bayanta aka fara gargada kowa idonsu a rife basaji basa gani dan bama asalin securities na gidan bane bare kaga sauki ko damar nuna matsayinka.

Kowa makaminsa aka sakasa sake dauka aka dinga turasu mota hadda Sayd sbd kowa da kowa akace dan haka babu ruwansu ko Mama rufe ido sukai suka bude mata motar.

Madam Sisi da Fiddausi tace ita ta fara ihun talla mata mari daya daga cikinsu yay Yana cewa

"Zakaci uban bakinka"

Fiddausi da Falaq da Jannah se Amina kadai aka bari sai me gidan kansa da tinda ya bada umarnin yabar gurin Yana samansa kishin Jannah zai kashesa sbd zuciyarsa dake jin zai iya illata Ammar har abada akan kalmarsa ga matarsa.

Falaq ce ta dakatar dasu daga tafiyar sbd tasan kwata kwata daddynta baya hayyacinsa ya bada umarnin dan haka idan ya dawo hayyacinsa zai tsani kansa har abada akan hakan ace shine ya bada umarnin aka rufe hadda mahaifiyarsa da mahaifin jannarsa dan haka bazata bari ya dandani wannan dacin ba.

Samansa taje tayi tayi tagansa Amma shiru bama ya palon yana bedroom dinsa Wanda ta tabbatarda ba lafiya ba.

Tsoro ne ya kamata dan haka ta sauko da sauri taje gurin Jannah da batama San an tafi da kowama ta sanar mata.
#MAMUH
#LIMBAS
#ZAADENS

#4&4
#PSCHS

07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 33

*_SHOP WITH ME BY RANO_*
08030811300
Kina neman in da zaki samun kayan yara classy kaya na yan gayu at a very affordable price? Ko kina son fara kasuwancin kayan yara amma baki da jarin da zaki saro kayan? Nesa ta zo kusa, kiyi joining community din nan muna saka kaya masu kyau available da inganci a farashi me sauki da zaki dauka ki tallata har ki samu naki kema.
Burinmu shine kowacce mace ta samu sanaar da zata dogara da kanta.

**************
Daqyar ta iya zuwa inda yake din sbd ita kanta tasan zai tsani kansa sosai daga baya idan ya gane abinda yayi sbd tsananin son dayake wa mahaifiyarsa da kuma yanda itama yasan tana tsananin son mahaifinta.

Numfashi ta ajiye tareda ajiyan zuciya ta miqa hannu akan kofar bedroom dinsa ta bude Falaq na komawa palon qasa dan jira.

Duhu ne a dakin dan haka ta isa gurin haske ta kunna ahankali tana juyo da idanuwanta ga dakin.

Kwance yake a tiles can bayan sofa ya qanqame jikinsa jikinsa na rawa sosai Yana yaqi da zuciyarsa dake illata tinaninsa,

Qarasawa tayi ahankali tareda durkusawa gefensa ahankali ta miqa hannuwanta duka biyun ta rugumosa tana kwantawa jikinsa ta lumshe idanuwanta hawayen cikinsu na sauka akan fatar wuyanta.

Qanqameta yayi kaman zai ballata ta rinse ido tana shanye azabar hakan sbd ta saba tin ba yanxu din ba sbd tasan lafiyansa sai ta koyi hadiyewa.

Qanqameta yake sakeyi da karfin da azabar take mata yawa Amma bata iya kwacewaba ko magana sbd tasan relief din dayake samu da hakan.

Shiru sukai a jikin juna tsawon minta ya samu sassaucin zuciya da jiki.

Ahankali ta bude baki tace

"Zasu tafi dasu Dad da Mama ka dakatar dasu pls"

Shiru yayi idanuwansa a rufe har lokacin,

Wayarsa ta tashi ta dauko masa tareda zaunawa ta kamo hannunsa ta saka masa a ciki tana kallansa cikeda tsananin abinda takeji a zuciya bakinta yana kasa furtawa.

Shiru tsawon lokaci kafin ya daga wayar Yana miqewa tsaye yabar gurin Yana nufar balcony dinsa ya tsaya.

Jannah ma miqewa tayi ta fice daga dakin ta sauko a sanyaye,

Falaq na ganinta ta taso tareda riqe hannunta tana kallanta kaman zata cinyeta sbd kauna tace

"Is my daddy ok?

Numfashi Jannah ta sauke ahankali tana dagowa ta zubawa Falaq din idanuwanta tsananin kaunar Falaq din na taso mata.

Falaq ma ganin hakan sake riqe hannun Jannah din tayi tana cewa

"My Jan,
My Dad's Jan"

Rungumeta Jannah tayi tana cewa

"I love you my baby"

Shigowan Sayd palon ce Kansa a qasa ya saka Jannah sakin Falaq tana kallan kofar alaman an sake kowa.

Qarasa sakin Falaq tayi tana barin palon ta kofar AZIZ tana isa harabar gidan inda bata tarar da kowa ba.

Bangarensu ta nufa da sauri tana jin jikinta na sake sanyi.

Da garba ta fara cin Karo Yana ganinta ya tsareta da ido Yana ransa inda komai ma na rayuwarsu data mutan gidan ta dosa.

Maheer da Dad ta sama suna kokarin shigewa da sauri ta iso gurinsu tana Kiran sunan Dad

bata tsaya komaiba ta fada jikinsa tana fasa kukan kunyar dake neman kasheta ta hau bayanin babu abinda ya hadata da AZIZ din kawai ganinsa tayi ita kuma tsoron ihun da ake ya sakata jansa ta boye ciki sbd ta dauka Ammar ne kada ayi masa sharri.

Ammar dake tsaye zuciya na son kashesa jin Ashe shi taje karewa take zuciyarsa tayi sanyi Yana sake jin sonta na cike koinansa.

Dad ma da Maheer da dukkaninsu koyaushe kaunarta ke rufe idonsu akan komai na rayuwa ydda sukai da zancenta suna tsake tsanar AZIZ din akan basusan niyarsa ta zuwa kofar dakin su Jannah din da dareba dan haka gabaki daya jin sukai sun sake tsanarsa da tsanar zama a 4&4 din akan a taba mutuncin Jannah sun zabi yafe Sanin inda Saleem yake zasu bar mansion din kota halin yaya ne.

Jannah data samu sassaucin nauyin kirjinta ganin sun amince da zancenta numfashi da ajiyan zuciya ta sauke ta dago ahankali tace

"Ina Ummah??

Gabaki dayansu daki suka kalla
Dad ya sauke numfashi me sanyi cikin nutsuwa da Yar damuwa yace

"Batajin dadi sosai sai asubar ma ta samu yin bacci bayan Tasha magani shiyasa inaga bata farka ba haryanxu abarta ta samu hutu yanda ya kamata.

Ammar ne ya bude baki yace

"Ko zaa kaita asibiti ne Dad sbd Ummah fa bata baccin safe har haka"

Girgiza kai Dad yayi yana qin kallan ko wannensu ya juya Yana cewa

"Zata farka Lfy kalau inshallah"

Jannah ma kaman munafuka ta juya dakinsu ta shige tana shiga ta zube qasa tana jero ajiyan zuciya da numfashi tana dafe kirjinta da bugawarsa ayau ta kusa tada ciwon data jima bataiba.

Fatma datai sallah take tsaye tsuru tsuru tana jiran Jannan sbd tasan ta kwafsa Amma kuma batai tinanin su bane tinda ko a mafarki bata taba tinanin AZIZ LIMBA a bangaren masu aiki ba bare dakinsu.

Jannah bta iya cewa fatma din komaiba toilet ta wuce ta sakarwa kanta ruwa tayo wanka ta fito zauna tareda kallan Fatma da zatai magana ta katseta da cewa

"Fatma pls kada kice komai nima haryanxu ban gama dawowa daidaiba abar abinda ya wuce

kawai banason Tina wannan masifar ta yau"

Shiru fatma tayi tana sake jin kunya na rufeta itama na yau din.

*********Da taimakon fiddausi Mama ta isa dakinta ta zube qasa tana son fasa ihun kuka amma girmanta ya wuce hakan hakama radadi da wutar dake cin zuciyarta ya hanata komai bare iya cewa komai,

AZIZ dinta ne ayau a bangaren masu aiki a cikin dakin Jannah?
AZIZ dinta ne idonsa ya rufe akan mace ya hadata da Zaadens ya zuba a motar karfe?
Idan AZIZ zai mata haka akan wata macen mezai faru idan yaga Fatima?
Menene kuma bazai iyayiba akan fatima?
Wlh tallahi wannan ba AZIZUN ta bane dan har abada AZIZ bazai taba take doka da umarninta ba bare tattarasu a zuba a mota kamar wainda aka kamo gidan gala,

Wlh da sake dan kuwa tana buqtaan tashi da tsayen gaske dan kwato danta daga hannun kowa da kuma hanasa shiga hannun kowa koda zata zama zarrriya ne.

Miqewa tayi daqyar takai kanta bathroom tayo alwalar asubar da basuyiba suka ari hauka suka tada anguwa.

Nicky kuwa tana shiga dakinta wani mahaukacin ihun ta fasa tana fasa kayan dakin da karfi cikin tsananin hauka da wata masifar wuta dake ci a kirjinta tana tafarfasa jininta.

Hannuwanta da wasu sassan jikinta jini sukeyi sbd yanda take fasa komai da hannuwanta ga glasses tana kukan baqin ciki batareda ya damu da jinin ba.

Dayake kowa yasan yanayin nata babu Wanda yayi yunqurin zuwa dakin shiru sukai Banda Falaq datake jin zuciyarta fes batajin sauran baqin ciki ko damuwar komai sbd Jan dinta data samu.

Duk sautin haukarta Bata isa bangarensa dan haka baisan mema Yan gidan suke ciki ba.

Dan kanta ta gama tayi laushi ta zube qasa tana kuka kaman ranta zai fita tanajin babu Wanda takeson rabawa da duniya irin Jannah da duka ahalinta ma.

Fatma da Amina ne sukai aikin abincin gidan wunin ranar sbd Jannah kasa fitowa tayi dakinta hakama madam Sisi da take a tsorace,

Su kuwa masu gidan kowa baqin cikin duniya ya hanasa fitowa cin abinci.

Fiddausi ce kadai ta sauko ta dauki abincinsu takai musu sama sukaci itada falaq hankali kwance.

Sayd ma ya fito dining yaci ya koshi ya koma dakinsa Yana ayyukansa.

Me gidan babu Wanda ya gansa har washe gari tukuna kowa ya samu danne abinda yake ransa suka hadu gabaki dayansu a dining hadda shi daya sauko a kame kyakkyawar fuskansa ba sakewa cikinta ko kadan.

Gaida Mama yayi a taqaice yana zaunawa,

Muhammad ne ya zauna kusa dashi yana kokarin rage Masa abinda yake ji ta hanyar cewa

"Inshallah daga Ammar har Dad zasu tashi cikin amincin Allah muyita fata da adduan hakan"

Maheer bai iya cewa komaiba sbd kansa da tinaninsa basa tafiya daidai kwata kwata a lokacin

fatan tashin Ammar da Dad kawai yake sbd samun nutsuwan sanin yanda zaiyi da Jannah.

Ummah ma Jannah dake kuka sosai har karfinta na neman karewa ta zaunar a gefenta kan kujera tana zuba mata ido tana sake karanceta tsaf ya tabbatar dai da ciki Kam akwaisa a jikin Jannah din Dan haka take jikinta yayi wani mugun sanyi sbd ciki a jikin macen da 'yayanta biyu sukewa tsananin so fiyeda rayuwansu ba qaramin illa da tashin hankali zai sakarwa rayuwansu ba ga Ammar nan ya shiga nasa halin bayan ya sani,
Saura AZIZ da batasan Shima Yaya zai ji lamarin ba wane halin zai shiga tinda dai ta tabbatarda yana tsananin son Jannah haryanzu duk da sun rabun tsawon shekara uku da akace mata a labari,

Yanzu ta ina AZIZ zai fara Jin zancen?
Yaya zuciyarsa zata dauka?
Shima zai iya shiga halinda Ammar ya shiga akan labarin koma fiye?

Shiru tayi itama nata tashin hankalin na ratsata sbd masifun basu qare ba kenan,
Abin tashin hankalin dayafi koma daga ina cikin ya fito?

"Daga kauye?????"  Shine abinda zuciyarta ta fara fada mata sbd daga can ta dawo ba lafiya Wanda tin lokacin ya kamata su gane Dan babu abinda bai sauya a jikin Jannah dinba me nuni da sabon ciki a jikinta,

"Innalillahi wainna ilayhirajiun" shine abinda Umman ta furta a fili tana dafe goshinta itama sbd Kanta dayake ciwon da kaman zai juye mata.

Shiru sukai dukkaninsu Banda Jannah datake ta kuka har muryanta ya dishe jikinta yayi wani irin zafi sosai zazzabi me karfin gaske yana shigarta dole fatma ta jata zuwa waje inda ta ringa wani irin wahalallen amai tana qarasa galabaicewa.

Qara tashi hankalin fatma yayi akan Wanda suke ciki sbd jikin Jannah din daya rikice mata lokaci daya gashi ta kasa dawowa ciki ta fadawa Maheer sbd a yanda take ganin wuta na cinsa ta bacin Rai zai iya musu dukan da cikinma zai bare Dan haka suka kasa dawowa ciki suka tsaya acan baya waje tana kokarin taimakawa Jannah din ta hanyar shafa bayanta Aman yana Dan tsayawa.

Miqewa Jannah ke kokarin yi Bata ma iyawa sosai zata koma ciki fatma ta riqeta tana cewa

"Jannah ki zauna anan kinga acan din ba iskan da zai ringa buga Miki Aman ya dena tahowa Kuma kin Dan matsa daga gaban Yaya Maheer da ransa yake a tsananin bace kada ya fusata ya Miki wani abin tinda bake daya bace.

Qin tsayawa Jannah din tayi sbd tafisan Maheer dinma ya kasheta akan tayi nesa dasu musamman yanzu datake ganin itace sanadin duka abinda yake samun familynta tin daga kan

ciwonta tin tana qarama ta gama zama kaddarar rayuwarsu gashi yanzu suna kwance suna kokarin rasa rayukansu sanadinta.

Miqewa tayi da Dan sauran karfin daya rage mata wani irin jiri ya debeta ta dawo baya zata fadi Fatma tayi saurin miqewa zata tarota Wanda ya iso gurin ta bayansu ya tareta jikinsa tana fada Masa gabaki daya shikuma ya saka hannuwansa ya zagayeta yana Bata kyakkyawan runguma a jikinsa batareda yace komaiba ya dauketa gabaki dayanta yana barin gurin da ita Fatma da Sayd na bayansa.

Wata hanyar yabi daban zuwa saman asibitin Wanda likitan daya kira da kansa yake jiransa ya nufa da ita idanuwanta na rufewa a jikinsa sbd ta mummunan gabalaitiwa kuka da tashin hankali sun cinye karfinta tas dana abinda yake cikinta.

Suna isa likita ya taso da kansa yana Masa barka da shigowa ya nuna Masa gado lafiyayye a wani dakin dayake saman ya kwantar da ita daman sayd da Fatma basu shigoba nan take likitan ya kira nurses guda biyu suka Taho take aka fara duba Jannah din Wanda yake tamkar a some Dan Bata iya ko bude idanuwanta.

Yanzu zaune riqe da hannunta cikin nasa aka fara dubata da sauran abubuwan har aka gama komai aka daura mata ruwa take bacci ya dauketa na wahalan gaske.

Scanning sabo Dr yayi masa na cikinta yana kallan Arzikinsa Dr na Masa bayanin dayake saka duniyarsa gabaki dayanta sanyaya da nutsuwan data Fi Masa komai na kyallin duniya.

Sake riqe hannunta yayi cikin nasa bayan angama komai nurses din da Dr sun fice ya zubawa fuskanta datai fayau idanuwansa yana kallanta kaman zai dauketa subar komai da kowa su tafi inda zata rayu a kwanciyan hankali itada babynsa su renesa babu hayaniyan komai da kowa.

Hannunta dake hannunsa yakai bakinsa yayi kissing cikin sanyi da tsananin kauna yana lumshe ido yanajin hankalinsa na kwanciya kawai ba ruwansa da tashin hankalin da kowa yake ciki.

Sayd da Fatma ne suka shigo suka nema guri suna zaunawa Dan taruwa a jinyar matar oga.

Shiru Shiru kowa na cikin nasa kalan damuwa da ciwon xuciya har akai Asuba tukuna dukkaninsu suka fita sallah,

Da LIMBA din dasu Maheer a masallaci daya sukai sallah amma Allah ba saka sun ga juna ba Dan haka suna gamawa kowannensu ya koma inda yake sai a lokacin Ummah da Garba suka ringa neman su Jannah wadda daga baya sukai tinanin sun koma gida da Fatma Dan haka suka ci gaba da zaman fargaba.

Sai guraren 8 na safe Dad ya farka dukkaninsu sukai private dakin da aka maidasa suna godewa Allah ganin shi ya tashi sauransu Ammar a yanzu Wanda dukkanin adduarsu ta koma

kansa kacokam.

Dad tinda ya tashin baice komaiba Shiru yayi radadin zuciyarsa na sake qaruwa kowace daqiqa har lokacin yana kasa yadda da masifar datake kokarin fado musu wai cikin haihuwan 'dan mutum a jikin Jannah,
Ta ina?
Ta Yaya?
Ba abu ne me yiyuba Dan yasan wacece Jannah bazata taba aikata barna ba Dan ba tarbiyanta bace,
Ba hali ko dabiun Banza datake dashi ko daya tin tana qanqanuwanta bare yanzu,

Jannah ko saurayi batada shi Bata kula kowa,shi kansa Ammar da zaayi musu auren bata wani sakewa sosai dashi a yanzu kaman baya sbd LIMBA daya cire mata dukkanin shaawan yin aure ko soyayyar datai a baya sbd abinda yai mata Dan haka tayaya Jannah zata dauki ciki ita kadai ba miji ba komai?

Shi kwata kwata bai yadda da ciki a jikin Jannah ba labari ne da zancen da yake neman kashesa da ransa kawai amma yana buqatan tabbatarwa Dan Kuwa badai cikin mutum ba sedai na iska.

Sake nitso a Shiru da tinani yayi nauyi kirjinsa na tsananta a ransa yace

"Kodai ciwon Fatima da Ammar bai gama warkeba yake kokarin dawowa suke tinanin ciki a tattare da Jannah daga tana malaria tinda suna tsananin kaunarta kawai kwakwalwansu ta basu wannan tinanin??"

Numfashi ya sauke me zafi cikin mutuwan jiki da sanyi yana dagowa ya Kalli Ummah dake gefensa cikeda tausayinta da kaunarta me karfi Dan baya kaunar ciwonta ya dawo ko kadan amma ga alaman Hakan nan Dan haka hannunsa ya Dora akan nata yana kasa cewa komai radadin zuciyarsa na karuwa sosai da qunci.

Umman ma cikeda kulawa da kauna ta dafa hannunsa daya Dora akan nata daya tana dagowa ta kallesa tace

"Dad ka dena saurin saka magana a ranka sbd gudun samun shock irin Hakan baida amfani komai tsananin lamari da muninsa sai an kwantar da hankali ake iya magancesa a warwaresa, Ammar yana kwance muna fatan tashinsa sai Kuma kaima ka saka mu cikin wani tashin hankalin Dan Allah ka cire komai a ranka Allah zai kawo mafita da sauki tareda maslahan komai na damuwan da mike ciki"

Shiru Dad din yayi yana gyada kai kawai kafin ya dago ya kalleta yana Dan kokarin dawo da nutsuwansa yace

"Yaya Ammar din??

Maheer ne ya basa amsa da cewa

"Sun gama basa taimakon gaggawa dayake buqata Shima ana jiran farfadowansa ne kowane lokacin"

Ajiyan xuciya me Dan sanyi Dad din yayi yana sake bude Baki yace

"Ina Jannah?

Kai tsaye Muhammad dake kokarin gyarawa Dad din pillow din dayake kokarin jingina daya tashi zaune yace

"Sun koma gida ita da fatma"

Shiru ne ya sake ratsa gurin kafin Maheer da kama Dad din zuwa toilet Dan alwala Ummah Kuma sake gyara Masa shimfidar gadon me Dan wali sosai tayi tana cewa

"Muhammad ka tabbata sun koma gidan ai ko??

"Insha Allah Ummah suna gida"

******Acan sai da gari yayi haske Jannah ta farka lokacin daga ita sai AZIZ din a dakin yana hannunsa da nata yana sarqe cikin lafiyayyan bargon da aka rufeta dashi Wanda sayd ne yaje ya kawosa sabo fil daga gida tin tsakar Daren.

Zubawa juna idanuwa sukai tana kallansa a sanyaye sbd har yanzu tashin hankalin Soyayyansa a rayuwanta bai qare ba sbd a yanzu da akasan tana dauke da cikin da bazata iya fadan nasa bane sbd kada a zubar mata da cikin wani babban qalubale da tashin hankali ne a rayuwanta data babynta da tinda ya bayyana sun sani tsananin son abinta takeyi sbd AZIZ LIMBA dinta ne ubansa,shine yabata kyautarsa datafi komai a rayuwanta yanzu,
Zata so ta haife Dan AZIZ LIMBA dake cikinta sbd sake basa farin cikin dazaifi komai na rayuwansa.

Shi kansa AZIZ din bazata iya fada Masa tana dauke da cikinsa ba sbd tashin hankalin yawa zaiyi idan yasan akwai ciki a jikinta kuma yaga familynta na kokarin daukan mataki akan laifin datai bazai kyaleba fitinar ahalin biyu tashi zatai ayita yi bayan saukinta da son zama abu daya datake fatan musu tsakanin LIMBAS da ZAADENS Dan haka Sai tagama karban hukuncinta sun karbi cikinta tukuna zata iya sanar dasu mahaifin cikin nata Shima ta sanar dashi.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*

Mamuhgee

Book 2
Chapter 65

*_ZUZEAM VENTURES_*
Best kayan Mata
08144015291
*NEW ALERT*
*END OF DISCUSSION PACKAGE*
~25k~ promo 12k
Barka da Sallah promo pack
1. Tabajen kankana da fruit
(Mai saukar da niima nan take ta kara miki dadi na musamman keda oga sai kunyi kukan dadi ranar )
2. gumbar chakwala dadi
(Hmm yar uwa daga jin wannan kema kinsani basai anbaki labariba wannan hadin na zallar dadi ne da ciko da gaba)
3. Turare kyauta dole
(Wannan turaren na amsar kyauta ne ina masu fama da miji mai mako wanda ba a cin kudinshi Ga shi da abun amma ba a ci to yar uwa matsalarki tazo karshe da izin Allah Sai kinci abunshi ina yan kasuwa duk kina amfani da wannan turaren sai Kinga budi da izinin Allah)
4. Zumar bata gaban kishiya yar asali
( wannan zumar Ga mata wanda kishiya ta shiga gabansu mijinki baki gane kanshi ya fifita yar uwarki akanki baya son mu’a mala dake ko wadda mijinta ke biye biye yar uwa kukanki yazo karshe duk kikayi amfani da ita duk machen da yayi sex da ita zaijita salab kamar dusa don haka aji tsoron Allah banda wanda suke zaune lfy da kishiyoyinsu)
5. End of discussion powder
( wannan garin karshen zance kenan hajiya oga ya taba miki kukan agwagwa ko mussoshi 😁to ranar duk da kika sha wannan hadin garin hajiya sabbatu sai kin rufe mishi baki ihu da kururuwa ba sauki kuma garin wata 7 yake ajiki yana aiki )

Hajiya karki bari wannan promo ya wuceki 25k ne promo saboda sallah 12k kacal

TikTok: Zuzeam.ventures5
Instagram: Zuzeam_ventures
WhatsApp: 08144015291

***********

"Hi Aslm alaikum Mrs LIMBA" shine abinda ya bude bakinsa cikin laushin murya da nutsuwa me sanyi ya furta can qasan maqoshinsa yana kallanta kafin yakai bakinsa yayi kissing hancinta yana Dan goga mata nasa hancin kan nata ya dago yana kallanta.

Bata iya cewa komaiba sai bakinta data bude kadan tace

"Meyasa kazo?
Su Dad zasu sake shiga fushi pls ka tafi banason kuyi wani damuwan fushi Kai da Dad"

Murmushi me sanyi ya sakar mata yana tayar da ita Zaune ahankali ya kama kafafunta ya sauko dasu qasa ya tayar da ita tsaye duka a natse kaman Wanda take cikin tsananin ciwo yace

"Muje ki fara tsarkake kanki da sallah tukuna"

Toile din dayake dakin kaman na tsadaddiyar hotel sbd tsari da kyansa ya shige da ita ya rufo kofar daidai nan Fatma da Sayd da fiddausi sai Falaq suka shigo dakin daga gida dauke da breakfast masu lafiya baske kusan uku da abubuwan buqatan Jannah din.

Da kansa ya taimaka mata tayi wankan tsarkin da bataiba tin jiyan sbd tashin hankalin da aka shiga tin acan ciki yace fiddausi ta kawo hand dryer da aka kawo da ita sbd yace a kawo da itan.

Da kansa ya busar mata da Kanta a toilet din kafin ta sauya kaya da kayan da Fatma tazo mata dashi tukuna ta fito tayi sallah shi Kuma Saida ya sauya nasa kayan Shima ya fito sbd wancan sun jiqe shikuma sayd daman baya wasa da komai na AZIZ a Shirye yake da kowane yanayin dazai kama Dan haka tin a cikin dare ya kawo kayan AZIZ din kusan kala uku sbd da safe koda babu abinda ya samu kayansa may b qamshin asibiti zaisa kayansa su ishesa ya buqaci sauya wasu.

Ko daya fito ta gama sallah da haka ya dago a sanyaye ta kallesa tana son cewa gurinsu Dad zata amma ganin duka wanda suke dakin basusan abinda yake faduwa ba yasata yin Shiru tana miqewa.

Breakfast akaso tayi ta kasa Sam gurin familynta take son zuwa dole ya hakura ya kyaleta.

Dukkaninsu suka isa dakin da Dad yake tana janyewa daga gefensa sosai ta koma gefe daya itada Fatma kaman tafiyarsu baa tare take ba musamman kallan da Maheer ke mata dad kuwa ko kallan inda take din baiyiba tukuna.

Ummah ce ta miqa mata hannu tana zaunar da ita gefenta Shima AZIZ din a dayan gefen Umman ya zauna yana kallan Dad bayan ya gaisa dasu Maheer kadaran kadaha ba sakewa ba Kuma basarwa.

Dad din ya yiwa ya jiki batareda yasan meya samesa ba amma dai kaman yanda sayd ma da baiji farkon draman data saka suman Dad dinba yace Masa shock ne na kasa dauka daukan halinda Ammar yake ciki ya sanyasa zubewa.

Ummah cikeda kulawa da kauna me sanyi take amsa gaisuwansa tana tambayarsa Mama.

Falaq ce ta amsa da cewa tana gida dayake tana zaune maqale da Jannah itama.

Dukkaninsu sunwa Dad fatan samun lafiya dashi da Ammar Kuma sun Dan jima kafin AZIZ da ahalinsa suka fice zuwa gida yana riqe da hannun yarsa dataso abarta gurin Jannah amma bazai iya Hakan ba sbd yasan suna cikin tashin hankali da damuwan Ammar ba zata gane kan Jannah dinba Sam ta bari kawai sai sun dawo gida.

Su AZIZ din na ficewa ummah ce tai karfin halin saka kowa yin breakfast akan dole na lafiyayyan abincin da aka kawo din Wanda daman dasu da Jannah da basuma San a asibiti ta kwana ba aka kawowa.

Sama sama kowa yaci abincin suka gama me gyara dakin ta shigo ta sake gyarawa tsaf ta daidaita ac ta sake cike dakin da kamshi ne sanyi ta fice tana sake musu fatan Allah ya karo lafiya.

Shiru dakin ya dauka kafin Dad ya dago ya kalli Jannah wadda ta rakube gefe Kanta a qasa ta kasa hada ido da Dad din bare Maheer.

Numfashi ya sauke me zafi yana bawa zafin kirjinsa damar ficewa ya bude Baki yana kallanta yace

"Jannah?"

Dagowa tayi ahankali ta kallesa cikin mutuwan jiki tace

"Naam Dad"

"Jannah me yake damunki?
Wane ciwo ne yake damunki kiketa sauyawa koyaushe?
Menene gaskiyan abinda nake ji sbd kwata kwata na kasa yadda da maganar da ni banason furtata da bakina"

Shiru Jannah tayi tana kasa cewa komai gabanta na faduwa zufa na keto mata tako ina sbd batasan tayaya zata iya bude Baki ta furtawa mahaifinta cikina a jikinta ba bayan sunsan batada auren kowa akanta.

Maheer ne ya dago jajayen idanuwansa da tin jiya yake Jin kaman zai makance sbd ja da radadin da suke Masa ya kalleta ya bude bakinsa Dan Shima so yake yaji ya tabbatarda gaskiyanta bai gama yadda da maganar wai ciki ne a jikintaba Dan bama abu bane me yiyuwaba yace

"Tambayarki akai kikai shiru"

Sake Dan ja baya tayi tana sake matsewa gefen Ummah hawaye masu zafi na cikowa idanuwanta suna fara gangarowa take ran Maheer daya matsu su fita wannan banzan tinani Da maganar cikin sbd tana kashesa yace

"Magana zakiyi ko kukan Banza ne anan an tambayeki abu kinayi kaman munafuka"

Ummah ce ta karbi zancen da cewa

"Ya isa Maheer abi a hankali mana ai zatai magana dole"

Dawo da kallanta kan Jannah dake kuka sosai qasa qasa tayi ta dafata tana kokarin kwantar da murya sbd kada ta sake daga hankalin Jannah din tace

"Ummijan,menene gaskiyan ciwon dayake damunki fada mun naji kinji sbd kowa hankalinsa ya kwanta,
Ki duba kiga halinda Ammar yake ciki sbd Hakan,ki Kalli Dad ma yanda ya kusa shiga mummunan hali duka sbd Hakan mu kanmu kwana mukai cikin zullimi da rudanin xuciya duka sbd Hakan Dan haka fada mana gaskia kowa ya samu nutsuwa,

Kinga ni bazan taba yadda da wannan zancen ba sbd ina shadan Ummijan Dina,
Dad ma Sam bai yadda ba sbd yasan wace yarsa,
Ko Maheer ma ransa yana sake baci ne sbd kin kasa cewa komai so muke ki bude Baki kice ba Hakan bane shikenan fa"

Wani sabon kuka Jannah ta sake Wanda ya saka tsikar jikin Dad da Maheer tashi,
Dad din ya hadiye wasu yawun wahala yana neman sarkewa sbd alamu na neman tabbata akwai abinda yake faruwa da Jannah din Dan haka ya bude Baki zaiyi magana Jannah din ta sake fasa kuka tana cewa

"Dad kayi hakuri ka yafemun Dan Allah......

Wani lafiyayyan mari Maheer ya dauketa dashi Wanda tinda take rayuwarta baa taba marinta ba Dan haka ta gigice tana riqe Ummah da karfi sbd jinsa cikin kunnuwanta da Kanta suna Wani dauke wuta ta fasa wani sabon kukan jikinta koina yana rawa ta sake bude Baki zatai magana Maheer yayo Kanta Ummah ta riqesa tana cewa

"Ka bari tayi magana tukuna"

"Ummah hakuri take hadawa ba tambayar da ake mata zata amsa ba" Maheer ya fada yana jin kaman zuciyarsa zata buga.

Fatma data miqe tsaye jikinta na tsananin rawa sbd tsoro kasa kallan Maheer din tayi yana yi bayan ummah itama sai a lokacin Maheer ma ya lura da yanayinta ya tsayar da kallansa kanta yace

"Fatma fito kizo nan"

Cikin sauri muryanta na rawa tana sake boyewa bayan ummah tace

"Yaya Maheer banyi komaiba bansan komaiba babu ma abinda yake damunta inji likita"

"Nace ki fito kizo Nan Fatma"

Hawaye itama ta fara masu gudu tana cewa

"Yaya Maheer dan Allah kayi hakuri sharrin shedan ne"

Da sauri dukkaninsu suka kalleta xuciyoyinsu na tsinkewa Dad ya sake hade wasu wahalallun yawu

Muhammad ma Matsowa yayi yana fizgo Fatman daga bayan Ummah da karfi ya turata gaban Maheer din zatai baya Muhammad ya riqeta yana daka mata tsawar data sakata tsayawa jikinta na Dan rawa tana kallan Maheer idanuwanta har lokacin suna hawaye.

Maheer da jikinsa ya fara mutuwa da maganar Fatman yace

"Fatma kikace sharrin shedan ne?
Ta ina shedan din ya biyo zaki mana bayani sbd kinsan komai"

Dad daya kasa hakuri da riqe tashin hankali bude Baki yayi yace

"Maheer ku kaita gurin likita yanzu Nan ya duba mana ita a gabanku kaida Fatima a kashe wannan zancen yayi nauyi"

Jannah na Jin Hakan ta sake sunkuyar dakai tana sabbin hawaye.

Gaba Maheer da Ummah suka sakata har scanning room dake asibitin Maheer ya samu yayi yanda zaiyi yayi payment me tsada aka shiga dasu scanning din sbd babu card nata na asibitin yana gida.

Karan farko ana farawa likitar tace

"Masha Allah babyn is healthy inshallah"

Rufe ido Jannah tai da sauri hawaye na gangaro mata gefen ido sbd ganin yanda Maheer yayi mutuwan tsaye yana jiri ya dibesa yayi baya zai fadi ya dafa bango da sauri yana Jin kansa na juyawa.

Ummah ma Shiru tayi tana zubawa Jannah din ido cikeda matsanancin mamaki harma batasan sanda tace

"Doctor cikin mutane ne Kuwa?
Kodai wani abin ne me kama da ciki kika gani?

Murmushi doctor din tayi tana cewa

"No,ciki ne lafiyayye wata uku a jikinta yanzu harda kwanaki ai kaman nai mata wani scanning din kwanakin baya data zo"

Shiru sukai babu Wanda ya sake cewa komai har aka gama suka fito takardar na hannun Maheer daya mata wata irin damqar da idan kaza ce data mutu.

Suna isa dakin Dad daga Dad din har Muhammad suna tsaye Fatma na zaune gefe zuru itama.

Rufe dakin Maheer yayi yana kasa kallan Dad sbd sanin zancen zai sake tabasa.

Ummah ma cikeda tausayi da kulawa take kallan Dad din Wanda tin a yanayin yanda suke kallansa ya sare ya miqawa Maheer hannu ya karbi scan din ya bude yana dubawa.

Jiri ne me karfi ya dibesa ya zaunar da karfi bakin gado sukayo kansa da sauri suna ambatar sunansa ya rintse idanuwansa jikinsa na rawa ya sauke kai yana cewa

"Innalillahi wainna ilayhirajiun,
Jamaa wannan masifar Kuma daga ina?

Ummah data kasa magana itama ajiyan xuciya ta sauke cikin sanyi da nutsuwa tace

"Ummijan daga ina?
Garin Yaya Hakan ta faru?

Fatma Maheer ya zubawa ido yace

"Kece me bakin bamu amsa yanxu saiki mana bayani"

Garba Kuwa cikin zafi yace

"Itama ai kaita yakamata ayi a dubata sbd tare suke komai"

Kuka Fatma tafashe dashi tana cewa

"Wlh tallahi Banda komai a jikina itama akwai aure ne a tsakaninsu"

Salati muhammd ya dauka yana cewa

"Kenan dai kinsan komai din Fatma?

Maheer Kuwa wani zufa ne ya fara jiqasa ya Kalli Dad Shima Dad din shi ya kalla suka Maida kallansu akan Jannah a tare tashin hankalinsu na tsananta Ummah da Bata gane inda zancen ya dosa ba sai ta karba zancen da cewa

"Indai akwai aure a tsakani Kuma su modibbo dake kauyen sun sani ai da sauki a lamarin" a tinaninta acan kauye akai wani auren.

Dad da Maheer Kuwa babu Wanda ya sake cewa komai sbd tsoron ma Jin abinda zai buga xuciyoyinsu Kuma ga Ummah a zaune basason fada ko nuna bacin ran da zai sosa ranta Dan haka sukai Shiru zufa na jiqa kowannensu amma tabbas suna buqatan zama na musamman da Jannah kafin suyi bikin kusan binneta da ranta.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 66

*_ZUZEAM VENTURES_*
Best kayan Mata
08144015291
*NEW ALERT*
*END OF DISCUSSION PACKAGE*
~25k~ promo 12k
Barka da Sallah promo pack
1. Tabajen kankana da fruit
(Mai saukar da niima nan take ta kara miki dadi na musamman keda oga sai kunyi kukan dadi ranar )
2. gumbar chakwala dadi
(Hmm yar uwa daga jin wannan kema kinsani basai anbaki labariba wannan hadin na zallar dadi ne da ciko da gaba)
3. Turare kyauta dole
(Wannan turaren na amsar kyauta ne ina masu fama da miji mai mako wanda ba a cin

kudinshi Ga shi da abun amma ba a ci to yar uwa matsalarki tazo karshe da izin Allah Sai kinci abunshi ina yan kasuwa duk kina amfani da wannan turaren sai Kinga budi da izinin Allah)
4. Zumar bata gaban kishiya yar asali
( wannan zumar Ga mata wanda kishiya ta shiga gabansu mijinki baki gane kanshi ya fifita yar uwarki akanki baya son mu'a mala dake ko wadda mijinta ke biye biye yar uwa kukanki yazo karshe duk kikayi amfani da ita duk machen da yayi sex da ita zaijita salab kamar dusa don haka aji tsoron Allah banda wanda suke zaune lfy da kishiyoyinsu)
5. End of discussion powder
( wannan garin karshen zance kenan hajiya oga ya taba miki kukan agwagwa ko mussoshi 😁to ranar duk da kika sha wannan hadin garin hajiya sabbatu sai kin rufe mishi  baki ihu da kururuwa ba sauki kuma garin wata 7 yake ajiki yana aiki )

Hajiya karki bari wannan promo ya wuceki 25k ne promo saboda sallah 12k kacal

TikTok: Zuzeam.ventures5
Instagram: Zuzeam_ventures
WhatsApp: 08144015291

*********
Nurse ce taxo ta sanar dasu Ammar ya farka Dan haka miqewa sukai dukkaninsu suka fice zuwa gurinsa har lokacin zufane ke jiqa rigarsa sosai yana Jin kaman jininsa na hawa yana qara hawa.

Maheer Kuwa rasa tinanin yi yayi sbd dai ta gama tabbata ciki ne a jikin Jannah yanzu Kuma tana sake Shirin tabbata cikin na AZIZ LIMBA ne ko me?

To tin sunada aure a baya aka samu cikin ya boye ya kwanta se yanzu yake bayyana ko me sbd baiga ta inda AZIZ din zai iya lalata musu 'ya ba harda ciki,
To yaushe ma akai Hakan?
Suna ina ne su harya samu kebewa da ita bayan sun kasa sun tsare sun Hana haduwansu bare alakarsu.

Idan cikinta wata uku ne ai a lokacin tana kauye kenan.....

Wani numfashi me zafin gaske ya sauke yana Jin yana buqatan karya kafafun Jannah da Fatma din kafin yaji komai Dan Kuwa wlh sai anfada Masa tayaya ma zaace AZIZ LIMBA ne uban 'dan cikin Jannah.

Dakin Ammar din suka iso Dad na tinanin da Maheer ke yi suna shiga suka watsar da tinaninsu suna qarasawa gurin Ammar din da sauri Wanda yake zaune Shiru ya zabge yayi fayau a Dare daya kaman ba Shiba,

Ummah ya zubawa idanuwansa wadda ta iso gurinsa tana zaunawa gefensa ya ciro hannunsa

ahankali cikin rashin kuzari ya miqa mata ta kama cikeda kauna da kulawa tana Jin idanuwanta na cikowa da hawayen tausayinsa,

Shi kansa cikowa idanuwansa da sukai jajir sukai yana Jin inama kowa zai hakura ya bar Masa Umman ya tafi ya Gina sabuwar rayuwa daga shi sai ita sbd ya gaji da komai a yanzu Kam hutu da nutsuwan ruhi na kwanakin da suka rage Masa yake nema.

Dad da Maheer zuba Masa idanuwa sukai cikeda tsananin kulawa da kauna me karfi suna Jin jikinsu na sanyi da yanda ya kasa kallan ko daya daga cikinsu idanuwansa na bayyanar da gajiya da gazawa da rayuwan gabaki dayanta.

Dad ne ya qarasa yana zaunawa dayan gefen Ammar din ya dafasa a natse yana bude Baki yace

"Ammar Yaya jikin?
Ka bamu tsoro da halinda ka shiga,Allah ya karemu daga sake ganin irin wannan mummunan yanayin"

Cikin sanyin da ya saka jikin kowa sanyi da mutuwa Ammar din ya bude Baki a natse da qaramin sauti yace

"Amin"  daga amin din bai sake cewa komai kaman yanda kowa ma yayi Shiru ya kasa cewa komai Saida Shirun yayi yawa Maheer Shima ya matso yana Masa sannu yana kallan fatma yace

"Hada Masa abinda zaici kafin yayi brush da sallah."

Miqewa Fatma tayi da sauri tana komawa dakin da Dad yake ta dauko basket na abincin da aka ajiye sbd Ammar din.

Maheer Kuwa shine ya kama Ammar din Wanda baida karfi sosai sbd karfin nasa bai dawo ba suka shige toilet.

Brush da wanka Ammar din yayi da ruwan zafi masu zafi jikinsa ya sake karfinsa ya Dan dawo ya goge jikinsa da towel din da aka kawo Masa tareda kaya tin daga gida ya saka riga da wando mara tsayi ya fito yayi sallah duka a natse ya koma bakin gadonsa ya zauna sai a lokacin ya dago ya zubawa Jannah idanuwansa yana kallanta batareda yace komaiba,

Jannah da tinda ta shigo ta kasa kallan Ammar din kunya da takaicin Kanta take ji data basa hope a karo na biyu bayan zuciyarta Bata cire Wanda shine yake cikeda ita ba gashi yanzu sun sake dawowa inda suka bari a baya ciwonsa zai iya tashin da zai sauya rayuwansa gabaki daya.

Dad da Maheer tsoronsu ciwon Ammar din dazai tashi daya sake tabbatarda da gaske cikin ne a jikin Jannah,

Abinda basu sani ba Ammar din ya riga yama San waye uban cikin sbd ya ga Hakan da idanuwansa da baya buqatan Jannah ta bude Baki ta fada waye me cikin,

Ajiyan xuciya me sanyi Ammar din ya sauke yana dauke idanuwansa daga kan Jannah din ya koma baya ahankali ya kwanta yana rufe idanuwansa Ummah ta rufe Masa jikinsa tana Hana kowa damunsa sbd babu abinda yakeso a yanzu kaman Shirun.

Haka sukai jigum jigum Shiru babu me abin fada zuciyoyi babu dadi Daci da ciwon Rai zalla tako ina.

Jannah ce ta zame tafice dakin ta koma waje ta zauna tana dafe goshinta sbd Kanta dake neman bugawa sbd a dakin Shiru kawai kowa yayi amma itace duka sanadin bacin Rai da quncin kowa tin farko haryanzu da ake cikin wannan halin.

Haka suka wuni a asibitin babu wani magana me Kyau dake shiga tsakanin junansu gabaki daya sbd Ammar kwata kwata bayason magana baya son rabar kowa bayason kallan kowa zuciyarsa tayi sakayau bayajin nauyin ko ciwon komai haka yake jinsa kaman sabon mutum din da aka Halitta ayau din,

Baya ganin laifi ko Jin zafin kowa kawai kansa ne yake gani Mai laifin daya kasa bawa zuciyarsa da rayuwansa damar samun sukuni da nutsuwan data kamacesa tin farko bayan rasa mahaifiyarsa,

Ya bari kunci ya mamayesa ya bawa duhu daman gauraye rayuwansa dayake ganin babu hasken dazai haskakesa saina Jannah da ahalinsa,
Ya rasa kowane irin hope na rayuwa da kwanciyan hankali da nutsuwansa ya kwallafasu akan macen da Bata taba Masa kallan masoyin daya sadaukar da kansa gaba daya akanta ba kallan Dan uwan da bazata taba iya zaman aure dashi ba take Masa gashi a karo na biyu ta sake zabar waninsa akansa Wanda a yanzu Kam komai ya qare yazo karshe take dukkanin abinda yake zuciyarsa yaji yana narkewa yana sauka daga kirjinsa Wanda a yanzu yake jinsa empty sbd Jannah ta riga ta zama macen AZIZ LIMBA Wanda ya gama mallakanta cikakkiyarta mace,

A yanzu Jannah Zad macen waninsa ce,
Jannah Zad a yanzu uwa zata zama wadda daga yanzu data dauki cikin wani ya gama samun iyakarsa da har abada ya tsaya anan bazai taba wucewaba sbd bawa rayuwansa daman samun sukuni da farin cikin daya rasa,

Ya sani haqqin Rai ne ke bibiyansa Wanda yake fatan zai samu nutsuwa ta hanyar yadda da Hakan sbd samun warwarewan damuwa da quncinsa daga ubangijinsa Dan haka Ayau shi

Ammar Zad ya hakura da dukkanin rayuwansa ta baya ya shafeta ya rungumi kaddararsa zai bawa kansa damar Dora sabuwar rayuwan daya kamata ya Dora tin a baya.

Da yamma Ummah da fatma da Garba suka bar asibitin suka koma gida Wanda ummah dole tayiwa Jannah na zuwa gidan suna isa gidan Ummah Bata iya barin kowama yasan mugun tashin hankalin Da suke ciki ba na ciki a jikin Jannah sbd ganin sirrinsu ne da bai kamata kowama yaji ba ciki Kuwa hatta AZIZ dayake danta da Mama datake uwar AZIZ din Kuma aminiyarta sbd ita tama Fi Jin kunya da baqin cikin AZIZ da mama suji sbd mutuncin Jannah din dazai zube a idon tsohuwar sirikarta da shi AZIZ din tsohon mijinta suji cikin da baa San ina ya fito bane a jikinta Dan haka sukai Shiru babu Wanda yasan me yake faruwa a cikinsu.

AZIZ na gidan bai fita koina ba daman jiran dawowansu yake idan Bata dawoba yana niyar tafiya asibitin ya dawo da ita gida da kansa sbd ita tama Fi Ammar din da Dad buqatan hutu da nutsuwa suda suke kwance a gadon asibitin amma itace ya kamata a bawa dukkanin kulawa ba su ba.

A dakin Ummah tayi wanka tai sallan laasar tana idarwa fiddausi takawo mata fruits da abinci ta lallabata taci fatma taxo da maganin da AZIZ din ya Bata tin a asibitin Wanda na Jannah ne ta ringa tabbatarda Tasha akan lokaci.

Maganin Tasha tana gamawa ta kwanta a farkon gadon Ummah tana dan lumshe idanuwanta tareda Dan rage AC.

Ummah na kitchen tareda su fiddausi da Kanta takeson ayi aikin abincin da Ammar zaici sbd gabaki daya ya kasa cin komai baya iya cewa komai Shiru kawai yakeyi yana sauke ajiyan xuciya akai akai tace ya yawaita ambatar Allah zai samu nutsuwan xuciya Dan haka duk ya numfasa saiya ambaci Allah Dan haka yaji yana samun sukuni da nutsuwan xuciya ahankali ahankali Dan haka ya  sake Jin baya buqatan yawan maganar Dan Hakan yana sakasa Jin yana sake dawowa daidai Wanda tin a shekarun baya ya kamata ace ya samu Hakan da kila baiyi batan da yayi ba a rayuwarsa.

Bude kofar dakin akai a hankali cikin nutsuwa tareda shigowa da sallamarsa me dadin sauraro ya rufe dakin qamshinta Dana AC daya gauraye dakin na shiga hancinsa take yasan tana dakin Umman Dan haka yakai idanuwansa bangaren lafiyayyan makeken gadon umman yana saukesu akanta.

Gurin Ummah yazo sanar da ita cikinsa dake jikin Jannah din sbd ta kula da ita a cikinsu Dad din da bacin Rai zai iya sakasu wani abinda zai taba lafiyan nasa arzikin sedai bai samu Umman ba yayi nasarar samun Jannah din data qi barin ya ganta tinda suka dawo kaman tasan neman zarewa yake rashin sanin halinda take ciki.

Qarasowa yayi har inda take din ya tsaya akanta yana zubawa kyakkyawan fuskanta nasa

fararen idanuwan yana kallanta kaman ya dauketa ya tafi duniyar dazai rayu da ita su reni babynsu.

Jin tsayuwan mutum a Kanta ya sakata bude idanuwanta ahankali tana saukesu akan fuskansa tana kallansa a kasalance sbd Dan zazzabi da rashin karfin dayake tattare da ita na Kukan datake yi tin jiya da Kuma damuwan data ciketa me tsananin rashin sanin wane hali da matakin familynta zasu dauka akanta da Kuma damuwan halinda ta saka Ammar Wanda kila qarasa rasa kansa zaiyi duk da ya kasa cewa komai ko kallanta bai sake ba.

Durkusawa yayi ahankali gabanta yana miqa hannunsa na dama ya shafi fuskanta cikin wata irin sanyayyan kulawa da kauna me tsafta.

Rufe idanuwanta ahankali tayi tana budewa akansa wasu hawaye masu dumi suna gangaro mata na tausayin Kanta da babynta da ubansa baima San dashi ba,

Idan su Dad sukace cire mata cikin zaayi batasan tayaya zata iya sake kallan AZIZ dinba duk da bai San dashi ba kaman yanda Kuma batajin zata musawa su Dad din sbd sanyaya zuciyarsu data kuntata,

Wasu zafafan hawayen ne suka sake sauko mata sbd tana kaunar cikinta har cikin ranta tana Kuma tausayin AZIZ da ita Kanta.

Hawayenta AZIZ din ya miqa hannunsa ya shafo yana kalla zuciyarsa na sanyaya da damuwa ya saka hannuwansa biyu ya tada ita Zaune ya dauketa yana komawa kan sofa da ita ya zauna ya zaunar da ita akan cinyarsa ya fara share mata hawayen da tissue daya dauka a gefen sofan dasuka zauna kan qaramin side table.

Hannunsa ta riqe da nata tana kallansa jikinta a sanyaye zuciyarta na ingixata akan ta fada Masa abinda take dauke dashi amma tana shakkar fushin su Dad idan suka San ta fada Masa Dan haka ta zuba Masa ido tana sake tsiyayan hawayen damuwa.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 67

*_ZUZEAM VENTURES_*
Best kayan Mata
08144015291
*NEW ALERT*
*END OF DISCUSSION PACKAGE*
~25k~ promo 12k

Barka da Sallah promo pack
1. Tabajen kankana da fruit
(Mai saukar da niima nan take ta kara miki dadi na musamman keda oga sai kunyi kukan dadi ranar )
2. gumbar chakwala dadi
(Hmm yar uwa daga jin wannan kema kinsani basai anbaki labariba wannan hadin na zallar dadi ne da ciko da gaba)
3. Turare kyauta dole
(Wannan turaren na amsar kyauta ne ina masu fama da miji mai mako wanda ba a cin kudinshi Ga shi da abun amma ba a ci to yar uwa matsalarki tazo karshe da izin Allah Sai kinci abunshi ina yan kasuwa duk kina amfani da wannan turaren sai Kinga budi da izinin Allah)
4. Zumar bata gaban kishiya yar asali
( wannan zumar Ga mata wanda kishiya ta shiga gabansu mijinki baki gane kanshi ya fifita yar uwarki akanki baya son mu'a mala dake ko wadda mijinta ke biye biye yar uwa kukanki yazo karshe duk kikayi amfani da ita duk machen da yayi sex da ita zaijita salab kamar dusa don haka aji tsoron Allah banda wanda suke zaune lfy da kishiyoyinsu)
5. End of discussion powder
( wannan garin karshen zance kenan hajiya oga ya taba miki kukan agwagwa ko mussoshi 😁to ranar duk da kika sha wannan hadin garin hajiya sabbatu sai kin rufe mishi baki ihu da kururuwa ba sauki kuma garin wata 7 yake ajiki yana aiki )

Hajiya karki bari wannan promo ya wuceki 25k ne promo saboda sallah 12k kacal

TikTok: Zuzeam.ventures5
Instagram: Zuzeam_ventures
WhatsApp: 08144015291

***********
Fuskansa ya hade da tata yana goga hancinsa da nata yana kokarin rarrashinta ya bude Baki da wata irin sanyi yace

"Pls Jan bana iya ganin wannan hawayen naki"

Maganarta ta Santa kuka me sauti xuwar mata tana fadawa jikinsa gabaki daya tana Jin ita kamarma Rabasu zaayi.

Rungumeta yayi tsam jikinsa yana qanqameta yana Jin kaman ya tsaga jikinsa ya maidata ciki ya rife abarsa.

Kuka takeyi sosai tana fada Masa itace sanadin duka damuwa da quncin danginta..

Dago fuskanta yayi yana sake share mata hawaye yace

"Ba haka bane karki manta su kansu fada sukeyi kece farin ciki Kuma wadda suke alfaharin tsananin son dasuke Miki ne ya riqe ahalin zaadens har babu Wanda ya isa ya raba wannan kaunar,

Aurena da soyayyata akanki bazata taba raba tsakaninki da familynki ba sbd karfin kaunarku a tsakaninku ta wuce nan ni kaina na San Hakan,

Duk bacin Rai da abinda zai faru a tsakaninku bazasu taba tsana ko kyamatarkiba sbd kece zuciyarsu da suke jure komai na rayuwa da suka fuskanta akanta"

Zuba Masa ido tayi sbd Jin maganarsa na ratsata Dan ita Kanta kaunar datake musu ce ta saka take shakkar bayyanarda aurenta da AZIZ din haryanzu Wanda Shima sbd tsananin son dayake mata ne yabi umarnin yanda takeso na boye Hakan ya Bata lokacinda ta buqata isashe tinda dai bawai rabasa tayi da Kanta ba.

Ganin irin kallan datake Masa hawayenta na tsayawa ya sakasa saka tissue ya qarasa share mata hawayen yana kai bakinsa yayi kissing idonta ahankali kafin yayi na hancinta tukuna yayi na bakinta yana sake zagayeta da hannunsa daya.

Kallansa tayi tana kokarin bude bakinta tayi magana ya Dora yatsarsa a akan lips dinta yana girgiza Kai a natse yace

"Kin gaji pls ki huta karki sake wahalan da kanki"

Hannunta takai akan nasa tana janyewa ta ce

"Idanma Ammar ya fada musu meyake faruwa pls kamun alkwarin baza Kai interfering ba"

"No,i can't make a promise da bazan iya cikawa ba"

Kallansa tayi tana ciko idanuwanta da hawayen da tasan zasu iya sakasa yadda zatai magana ya Dora bakinsa a kan nata yayi kissing nata sosai kafin ya saketa yana kallan fuskanta hannuwansa tallafe da fuskanta yace

"Bazan taba iya Miki alkwarin tsayawa nayi Shiru ina kallan ana min wasa da Arzikina na duniya ba"

Hawayen ta sake tsiyayowa yana share mata yana kissing idanuwanta da hancinta yana kokarin hanata wannan hawayen da duk ya damesa.

Kokarin sake kissing lips dinta yakeyi aka bude kofar dakin da suka manta da inda suke kwata

kwata.

Saurin janyewa Jannah din tayi jikinta na tsananin rawa ta miqe da mugun sauri daga jikinsa tana komawa bakin gado da gudun gaske har tana bigewa ya miqe tsaye yana kallanta da mamaki yace

"Kibi a hankali fa"

Ummah data shiga mummunan shock da firgita duk rikicewa tayi tana qarasowa tareda yi kaman bataga komaiba sbd ta kasa ma gane me idanuwanta suka ganar mata.

Rawa hannuwanta ke yi ta qaraso tana amsa gaisuwan AZIZ batareda ta iya kallansa ba hakama Jannah din Dan haka kai tsaye toilet ta wuce tana shigewa bayan tayi Masa Saida safe alaman batason fitowa ta samesa a dakin.

Tana shigewa ya qaraso ya durkusa yana duba kafan Jannah din data bige tayi saurin janyewa tana cewa

"Ka tafi kada Ummah ta sake fitowa ta ganka"

Kamo fuskanta yayi bayan ya miqe ya Dan rankwafo yai kissing goshinta yayi mata sai da safe ya fice.

Bai wani jima da fita ba Ummah dake bathroom tana faman sakawa da warwarewa cikin fargaba da tashin hankali ta fito tana qarasowa ta zauna har lokacin ta kasa kallan Jannah wadda ta kwanta ta lafe Shiru kaman tana bacci itama sbd kunya da tata fargaban data rufeta na tsoro da fatan Ummah Bata gansu ba.

Shirin bacci Ummah ta miqe tayi tana Jin kamar zazzabi na neman kamata sbd Bata fatar wani sabon tashin hankali a tsakanin AZIZ dinta da Zaadens da suke ahalinta a yanzu.

Gama komai tayi Tazo ta zauna bakin gado tana kallan Jannah wadda yanda take numfashi da motsi ahankali ya tabbatar mata da idanuwanta biyu ba bacci takeyi ba.

Cikin nutsuwa da sanyi Umman ta bude Baki ta ambaci sunanta tace

"Ummijan tashi magana zanyi dake"

Jannah na Jin Hakan gabanta yayi mugun faduwa tana Jin zufa na kokarin yanko mata amma ta riga tasan Ummah bazata taba fushi me muni da ita ba Dan haka ta juyo ahankali tana tashi zaune daga kwancen ta sauke Kanta qasa tana kasa hada Ido da Umman tayi Shiru.

Umman ma Shiru ya fara yi tana nazarin maganarta kafin ta fuskanci Jannan da Kyau ta bude

Baki a cikin nutsuwan da zata fahimceta dakyau tace

"Jannah nice na haifi ABDULAZIZ Dan haka bazan taba goge a cikina ya fitito ba sedai Kuma a yanzu ba nice uwarsa ba ba shine 'dana ba,

A yanzu kece tawa,kece 'yata dan haka ke nakeson ji daga gareki idan har na isa na Kai matsayin uwa a gurin ki Jannah inason sanin meyake faruwa tsakaninki da AZIZ,
Yaya akai kike dauke a ciki a jikinki?
Kuma na waye?
Ni duka banason ma furta wanna maganganun a bakina sbd Daci da nauyi sukemin Dan haka ki sanar Dani komai bana buqatan sake tambaya."

Numfashi me sanyi da mutuwan jiki Jannah ta sake a boye sbd daga karshe dai zata samu rage damuwan ranta Kuma daman batada Wanda zata iya fadawa damuwa da abinda tayin bayan Ummah Dan haka a Sanyaye ta bude Baki tace

"Ummah bai sakeni ba tin farko...

Da sauri umman ta kalleta tana sake shiga rudani tace

"AZIZ din ne be sake ki ba tin acan baya har yanzu da mike magana?

Gyada kai Jannah tayi
Umman tace

"To tin farkon waye ne yace anyi sakin?

"Ummah takarda ya bani bayan munyi maganar rabuwar shiyasa ban bude ba na sanar dasu Dad mun riga mun rabu......

"Da kika fada Hakan baa duba takardar bane daman kokuwa Baki bawa ko dayansu takardar ba?
Innalillahi me nake ji haka ni Fatima
Jannah kinsan me kika aikata Kuwa?

"Ummah wlh tallahi bansaniba nima sai daya fadamun naje na duba naga ba sakin bane Kuma na kasa fada ne sbd ina tsoron su Dad amma wlh ummah nima bansaniba"

"Innalillahi yanzu kenan cikin nasa ne ko me?"

Gyada kai Jannah tayi hawayen kunyar duniya na gangaro mata.

"Kikace nasa ne?

Kenan kallan kitse saman ruwa kuke mana tintini ko??

Sauti kukan Jannah din ya fara ta girgiza Kai tana cewa

"Aa Ummah Dan Allah kuyi hkr wlh sharrin shedan da zuciya ne"

"Wane shedan da zuciya baya ba aljanu ne a kanku ba"
Shi AZIZ din ya biye Miki Shima ya boye aure kenan,
Sai yaushe ne kuke da niyar fada kokuwa se dai idan an haihu mun ganarwa idanuwanmu"

Kuka Jannah ke yi sosai tana rokon Umman tayi hkr karta fadawa su Dad yanzu.

Fada sosai Umman ke mata akan irin kuskuren datai na boyewa familynta sbd ko zasu kama da wuta ya kamata Susan komai da duk baa ma fara yiwa cikin zargin ta ina ya fito ba.

Yanda Jannah din ke kuka tana rokon da Bada hakuri ya saka Umman sassauta fadan nata tana komawa rarrashinta tareda Jin nutsuwa da farin cikin samuwan cikin tinda dai jininta ne batada yanda zatai kota wace hanya yazo ma haka zata so sa ta kaunacesa.

Hakanan ta rarrasheta tana sake mata nasihar kiyaye gaba ta Hanata kukan hadda Bata ruwa Tasha tace ta kwanta tayi baccinta.

Sanyi da sassauci a kirji Jannah tace sbd ta samu rage nauyin kirjinta da samun tattaunawa da ummanta Dan haka Bata jima a tinani da damuwan sauran su Dad na bacci ya dauketa.

Ummah tinani ta kwana na yanda zata sanar dasu Dad cikin fahimta zata bari sai sun dawo hankali ya kwanta tukuna tinda da komai yazo da mafi girman sauki akwai aure Kuma na gida ne.

Washe gari Tinda safe suka tafi asibiti har lokacin Ammar yana Nan a yanda yake na bangaren magana ko wata hayaniya duk ya ajiye ya koma musu sabon mutum.

Sallamo su akai suka dawo gida,

Kowa dakinsa ya nufa yayi wanka yahuta babu Wanda ya sake ganin Dan uwansa sai dare da suka fito gabaki dayansu cin abincin da suke jiran ya hadasu Dan magana.

Karfe goma kowa ya watse Dad ya saka Muhammad Kiran Jannah da fatma Wanda suke boyo a daki sun kasa fitowa.

Kaman munafukai haka suka fito kansu a qasa suka nemi guri suka zauna sai a lokacin Dad ya qarewa Jannah Kallo zuciyarsa na neman fitowa sbd bacin Rai da tsananin fushi yace

"Ki bude Baki yanzu kimun bayanin komai dallah dallah sbd wlh tallahi kikamun qarya zakiga abinda Baki taba gani ba,
Cikin waye a jikinki?
Daga ina ya fito.?

Ammar dake zaune kusa da Dad din lumshe idanuwansa yay ahankali yana ambaton sunan Allah cikin sanyi da nutsuwa.

Maheer jajir idanuwansa sukai yana Jin baima San me zaiyi ba ta ina ma zasu fara da wannan abin kunyar da baqin cikin.

Kuka Jannah ke kokarin farawa Maheer yace

"Kina fara kuka wlh tsinannan dukan da zakisha saiya barar da abinda yake cikinki"

Sunkuyar da Kai tayi tana rufe bakinta da hannuwanta biyu muryanta na rawa tace

"Dan Allah Dad kuyi hkr wlh bansan da cikin ba nima.....

Kanta Maheer yayo Muhammd ya riqesa sbd basason hayaniya sbd kada kowa ya jisu bare asan halinda suke ciki musamman Ummah da ita ce nauyinsu a yanzu basason tasan abinda suke Shirin aikatawa idan ma zarginsu ya tabbata kenan.

Fatma ce ta karbi zancen itama cikin tsananin fargaba da hawaye tace

"Wlh Yaya Maheer akwai aure a tsakaninsu bai saketa ba tin farko can baya."

Cak Maheer din ya tsaya yana kallan Fatma da tsananin mamaki da shakka yace

"Wane auren ne be mutu ba?

Dad daya kasa hakuri a bada amsar Shima cikin tsananin shock yace

"AZIZ dinne bai saketa ba kokuwa wani auren tayi a kauyen bamuda labari??

Murya na rawa Fatma tace

"AZIZ LIMBA dinne baiyi sakin aurensa ba tin farko Kuma shine baban cik.....

Mari Muhammad ya yankawa bakin Fatman yana Jin kaman ya rufeta da dukan gaske yace

"Uban waye yake Baki wannan labarin??

Da sauri jikinta na rawa ta dauko takardar ta kawo ta miqa musu Maheer na karantawa ya zube a kujera zufa na jiqasa tako ina idanuwansa Kafe akan Jannah data Dora su a zancen Banza tsawon shekaru.

Dad na ganin Maheer ya zube ya kasa karantawa muryansa na rawa yace

"Da akwai auren kenan???

Ammar daya kasa motsi bare iya cewa komai bude jajayen idanuwansa da sukai wani irin jajir yayi ya katse tashin hankalin da nasa maganar yace

"Dad gobe nima zan tafi bazan iya cigaba da zama anan ba"
#MAMUH
07019691719

*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 68

*_ZUZEAM VENTURES_*
Best kayan Mata
08144015291
*NEW ALERT*
*END OF DISCUSSION PACKAGE*
~25k~ promo 12k
Barka da Sallah promo pack
1. Tabajen kankana da fruit
  (Mai saukar da niima nan take ta kara miki dadi na musamman keda oga sai kunyi kukan dadi ranar )
2. gumbar chakwala dadi
(Hmm yar uwa daga jin wannan kema kinsani basai anbaki labariba wannan hadin na zallar dadi ne da ciko da gaba)
3. Turare kyauta dole
  (Wannan turaren na amsar kyauta ne ina masu fama da miji mai mako wanda ba a cin kudinshi Ga shi da abun amma ba a ci to yar uwa matsalarki tazo karshe da izin Allah Sai kinci abunshi ina yan kasuwa duk kina amfani da wannan turaren sai Kinga budi da izinin Allah)
4. Zumar bata gaban kishiya yar asali
( wannan zumar Ga mata wanda kishiya ta shiga gabansu mijinki baki gane kanshi ya fifita yar uwarki akanki baya son mu'a mala dake ko wadda mijinta ke biye biye yar uwa kukanki yazo karshe duk kikayi amfani da ita duk machen da yayi sex da ita zaijita salab kamar dusa don

haka aji tsoron Allah banda wanda suke zaune Ify da kishiyoyinsu)
5. End of discussion powder
( wannan garin karshen zance kenan hajiya oga ya taba miki kukan agwagwa ko mussoshi 😁to ranar duk da kika sha wannan hadin garin hajiya sabbatu sai kin rufe mishi baki ihu da kururuwa ba sauki kuma garin wata 7 yake ajiki yana aiki )

Hajiya karki bari wannan promo ya wuceki 25k ne promo saboda sallah 12k kacal

TikTok: Zuzeam.ventures5
Instagram: Zuzeam_ventures
WhatsApp: 08144015291

********
A rikice suka kallesa a tare Maheer na rintse idanuwansa dake radadi sbd yasan Hakan zata iya faruwa tinda ganin yanayin Ammar din ya sauya ba kaman Ammar dinsu na bayaba.

Dad kuwa kasa dauke idanuwansa yayi daga kan Ammar din yace

"Ka tafi ina?
Kanada gurin tafiyan ne batareda familynka duka ba?

Sunkuyar dakai yayi yana sake tabbatarwa da zuciyarsa abinda rayuwansa ke buqata kenan yace

"Dad bazan iya rayuwan bane anan,
Ina buqatan sabuwar rayuwan da ko babu komai na kyallin duniya zan samu nutsuwa,
Kuma Dad a duk inda kuke ko bama tare ku family na ne bazan taba sauya Hakan ba sbd Banda uwa Banda uba bayan ku din Kuma Jannah dinma ina rokon tinda Allah yasa akwai aure Hakan ta faru a barwa Allah komai a rungumi kaddarar a yanda tazo amma nidai gobe insha Allah zan tafi koda kauyen ne zan koma sbd zan samu nutsuwa acan"

Shiru suka Jannah na fasa kuka tareda rarrafowa gurin Ammar din tana rokonsa Dan Allah kada ya rabu dasu bazasu iya rayuwa babusa ba.

Dad da Maheer Shiru sukai sbd lamarin Kuma ya juye yana neman raba tsakaninsu Wanda daman Hakan suke gudu shiyasa sukeson hada auren koyaushe sbd kada Ammar yaji shi bare a cikinsu Dan Kuwa shi nasu ne har abada.

Ajiye maganar Jannah akai dukkaninsu suka fara kokarin sauya raayinsa na tafiyarsa yabar cikinsu amma Allah yariga ya cire Masa komai a ransa sabuwar rayuwa yakeso a inda ba Nan ba koma ina ne.

Wannan tsayayyen raayin na Ammar shine sabon lamarin daya riskesu Wanda ya sakasu

yanke shawarar tafiya gabaki dayansu a taren washe gari batareda tinanin komaiba hakama maganar cikin Jannah sun rufeta a tsakaninsu babu me sanin tanada ciki zasu tafi suyi renansa ta haifesa kaman yanda Ammar ya roka ya Kuma bada shawara idan yaso daga baya ayi magana amma dai yanzu sbd Ammar din zasu tafi zasuyi Shiru suma kaman yanda AZIZ yasan basusan da maganar auren ba zasu fuske a Hakan sai sungama healing Ammar tukuna zuwa lokacin Jannah din ta haihu itama.

Ummah ma bazasu taba fada mata cikin AZIZ din bane a yanzu zasu rufeta sbd duka abar komai a rufe sai sun samu yanda suke son tukuna kome zai biyo ya biyo.

Da wannan suka kwana batareda bawa Jannah gargadi me karfin gaske na kada ta fadawa kowa komai har tafiyan.

Washe gari tin Asuba Ummah kaman ta sani ta Taho ta duba Jannah ta taddasu suna Shirin tafiya sai suka Dan boye mata sbd gargadin Dad da Maheer.

Kai tsaye Umman ta fahimci akwai abinda yake Shirin faruwa Dan haka ta nufi dakin Ammar Wanda yake kokarin kiranta a waya sbd bazai iya tafiya batareda yayi bankwana da ita ba.

A Palo suka hade yana ganinta sai a lokacin tinda abin ya faru yaji hawaye masu tsananin zafi sun ciko idanuwansa suna gangarowa tana qarasowa gabansa ya zube a kafafunta yana fasa wani irin kuka me tsananin karfi da wani irin tsananin ciwo da baqin cikin rayuwar dayayo a baya ayau gashi ya wayi gari baida kowa baida komai baida Wanda zai kalla yaji sanyi sai uwar daya kashewa 'ya da hannuwansa.

Wani irin kuka me ratsa xuciyan duk Mai sauraronsa yakeyi yana qanqame kafafun Umman wadda itama take kokarin hawayen tana Jin gabaki daya jikinta da zuciyarta na mutuwa akan Ammar din Wanda a yanzu ne lokacinda yake tsananin buqatan duk wani Mai kaunarsa Dan haka taji tana sake kaunarsa da tausayinsa.

Dad da dukkaninsu da suka fito sbd kukan Ammar din jikinsu tsananta sanyi yayi Maheer daya kasa riqe kansa sbd yanajin radadin da Ammar din yake ji har ransa kukan yakeyi Shima sbd jarabawan da Ammar yake ciki dole zasu runguma su bisa duk inda ta kama suyi rayuwan.

Dad ma Jin yayi yana hawayen gazawa a matsayinsa na uba daya kamata ya tsaya musu a komai ya Dora su akan hanyar data kamata gashi yanzu sun rasa alkiblarsu haryanzu basusan matsayin da rayuwa ta ajiyesu ba amma dai kaman yanda suka saba zasu runguma juna a kowane hali daman baya a kamata su tafi tin da dadewa Dan haka lokaci yayi na su tafin koda kauyen ne su koma sun Tara abinda zasu bawa Ammar da abinda Jannah zata Haifa rayuwa me Kyau.

Sun jima a wannan yanayin kafin Ammar din ya dago idanuwansa da sukai jajir ya Kalli ummah kallan bankwana ya bude Baki yace

"Ummah tafiya zanyi,
Zan tafi duk inda Allah ya nufa zan rayu Kuma,
Zan tafi Ummah,zan tafi.....

Kasa riqe Kanta Umman tayi itama kukan takeyi tana girgiza Masa Kai tana cewa

"Ammar kada ka tafi koina,
Babu inda zaka tafi Ammar."

Dad ne ya kalleta idanuwansa jajir Shima ya bude Baki yace

"Ba shi kadai ne zai tafi ba dukkanin mu ne zamu tafi"

Da sauri ta Kalli Dad din tana cewa

"Dukanku kaman Yaya?
Ina kuke maganar tafiya Dad??

Kallan yaran yayi Wanda sukai Shiru kowa zuciyarsa ba dadi.

Hannun Umman ya qaraso ya kama ya jata zuwa dakinsa a natse ya rufo kofar ya kalleta yana mata bayanin zasu sauya gurin rayuwa ne kawai sbd Ammar Wanda zai samu nutsuwa Dan haka idan tanada raayin cigaba da aurensa ta shirya zasu tafi tare idan Kuma batada raayi bazai taba mata dole ba.

Wani irin nauyi ne ya danne kirjinta data kasa cewa komai bayan Kafesa da ido tana Jin wani irin bacin Rai na taso mata amma Kuma bazata iya tsayawa fada dashi ba sbd kalamansa juyawa tayi ta fice daga dakin kawai.

Tana fitowa kai tsaye dakinta ta wuce ta dauki wayarta ta saka Kiran AZIZ Wanda baya gidan.

Wayarsa Bata shiga kwata kwata Dan haka ta saka Kiran sayd Wanda yana dauka ta sanar dashi Kai tsaye ya sanar da AZIZ din dake zaune yana wani meeting a laptop dinsa.

Katse meeting din yayi yana karban wayar ya miqe ya isa bakin window dinsa yana sauke ajiyan xuciya me sanyi yace

"Ummah ki barsu su tafi zasu tafi inda kowannensu zai samu nutsuwan da zasu samu damar tinani me Kyau harma a samu maslar komai,
Daman lokacin tafiyansu yai ko basu ce zasu tafi ba Mai tafiya dasu din yana gari ya sauka a jiyan,

Ummah Banda sauran damuwa ko wata gaba tsakanina da Zaadens sbd sune ahalin macen danakewa kallan itace rayuwata a yanzu Kuma ita da abinda yake cikinta sune arzikin da nake alfahari dasu Dan haka babu Komai ta bangarena Matiqar bazasu taba Matata da cikina ba Dan haka su tafi sbd itama Jannah din ta samu nutsuwan data rasa kwanakin nan a cikin familynta"

Ummah datake sauraronsa jikinta sanyi yayi sbd AZIZ din ya sake nuna mata zuciyarsa batada sauran tsatsar komai akan zaadens.

Ayau da Asuba yana dawowa masallaci ta gama tinkararsa da maganar Jannah da cikinta ta fahimta Kuma ta nutsu da yanda yake kaunar matarsa Dan haka itama tana bayan aurensa da Jannah.

Ajiyan xuciya Umman ta sauke tareda cewa

"AZIZ Allah yayi Maka albarka ya baka kariya da dukkanin abinda kakeso"

"Amin Ummah nagode"

Numfashi ta sake saukewa tace

"Bazan taba samun nutsuwan barin Jannah a cikin wannan halin da bacin Rai zai saka Dad da Maheer daukan matakin da bai kamata akanta ba sbd abinda yake cikinta Dan haka zan bisu har zuwa lokacinda zata haihu inshallah"

Murmushi me sautin nutsuwa AZIZ ya sake yace

"Ummah Jannah ai bazata haihu baa hannuna ba,
Na Bata daman daidaitawa ne da iyayen nata kafin karbanta,
Ummah bazan taba Baki zabi ba sbd inason kibi duk abinda zuciyarki take so idan har zaadens sune ahalin da zasu Baki nutsuwa ina Miki fatan alkhairi a cikinsu sbd nasan ko zuciyarsu ba Kyau ke suna Miki kaunar jininsu dake yawo a jikinsu Dan haka Ummah Allah ya Baki farin cikin da duk kike buqata a rayuwa ki bisu kawai sbd auren dayake tsakani"

Wasu hawayen tausayin dan nata ne suka cikowa idanuwanta sbd tana Jin karfin hali da tawakkali a muryansa dake fita cikin sanyin nutsuwa.

Dad ya Bata ranta sosai datake Jin Bata buqatan binsu amma kukan da Jannah ta ringa mata tana tsananin buqatanta ya sakata amincewa ta bisu sai Kuma Ammar datakeson tsayuwa a rayuwarsa taga bai sake nisa a duhu ba.

Gabaki daya gidan tashi hankalinsu yayi da tafiyan zaadens din Wanda babu Wanda yasan da ita Saida suka fito da komai nasu zasu wuce.

Falaq jikinta na tsananin rawa ta fito da gudu ta nufi Jannah ta rungume ta baya tana fasa kuka tareda qanqameta tana cewa zata bita.

Fiddausi da hawayen takeyi qarasowa tayi itama tana riqe Jannah din tana kokarin Kiran Sayd Dan ya sanar da AZIZ,

Mama ganin da Ummah zasu tafiyan tasu ya saka itama Hankalinta tashi batasan lokacinda ta isa gaban Dzad ba tafara rokonsa akan suyi hkr Dan Allah kada su tafi su bari AZIZ ya dawo.

Girgiza Kai dad yayi batareda ma ya iya Bata amsa ba.

Falaq gabaki daya ta daga hankalin duka Wanda yake gidan da kukanta ya riqe Jannah ta Hanata tafiya tana cewa a kira Daddynta cikin kuka.

Jannah data kasa kwacewa daga Falaq din sbd kukan takeyi itama tana Jin kaman zaa Rabata da zuciyarta ne barin AZIZ LIMBA da Falaq Aziz.

Maheer ne yazo ya fara kokarin banbare Jannah din daga Falaq wadda taki sakinta kuka takeyi sosai tana Kara kukanta dake fitowa daga zuciyarta sbd bazata iya rabuwa da Jannah ba a yanzu.

Fatma Maheer yasaka taja Masa Falaq din sbd ta zama yar budurwa ba huruminsa bane tabata shikuma yana kokarin Jan Jannah suka fara kokawan Rabasu fiddausi ma riqe Jannah din tayi Dan haka gurin ya rikice gabaki daya.

Tashi hankalin Dad yai sbd so yake suyi saurin tafiya kafin AZIZ ya dawo yasan abinda yake faruwa harma yayi kokarin hanasa tafiya da matarsa da daman rabuwa da ita tamkar barin ruhinsa ne a gidan Dan haka ya taho Shima ya fara Jan Jannah din wadda zuwa lokacin itama ta riqe Falaq sosai.

Rikicewa lamarin ya sake take hayaniya ta tashi a gurin sbd budar bakin Falaq cikin kuka cewa tayi

"Dan Allah kada ku rabani da Jan da babyn daddyna da zata Haifa mana muna tsananin sonsu ku tafi ku bar mana Jan ta haihu anan"

Dad na Jin Hakan take ciwon zuciyarsa ya fara kokarin tashi ya qara karfinsa gurin janye Jannah din sbd kada komai ya lalace idan AZIZ ya samesu gidan.

Mama dataji sauka zancen kamar saukar aradu suman tsaye tayi tana kallan Jannah da Zaadens din da rashin gaskiyansu ya bayyana a fili.

Cikin tata haukan data motsa itama ta fado cikinsu tana riqe Jannah itama tana cewa

"Sisi yi sauri saka mana Kiran Sayd idan an kasa samun AZIZ babu wanda zai bar gidan Nan sai AZIZ ya dawo"

Madam Sisi jiki na rawa ta fara saka Kiran sayd sedai Bata shiga Shima Dan haka tazo ta saka hannu itama tana riqe Jannah

Ganin haka Shima Muhammad yazo ya fara taya su Dad kokarin janye Jannah din.

Ummah data rikice ganin ana neman raba Jannah din biyu da zazzage cikin jikinta kowa baya hankalinsa sbd su Dad din idonsu ya rufe tafiya sukeson yi kota Yaya tinda maganar cikin ta bayyana su Kuwa su Mama sun kasa bari a tafi sbd AZIZ baya Nan kada su gudu da cikinsa Falaq Kuwa Jannah din gabaki dayanta take tsananin son da bazata iya rabuwa da ita ba tafison ta bisu.

Gate aka bude na biyu beymack din AZIZ baqa ta shigo wadda ta saka kowa dakatawa cikin tsananin halin farin ciki da baqin ciki ga zaadens.

Ganin yanda kowa yake kallan mota ana jiran fitowan AZIZ ya saka Maheer da Dad Jan Jannah da karfi suna nufar hanya cikin mugun sauri

Take su mama da Sisi suka bi bayansu da gudu zasu sake riqe Jannah Falaq data kasa motsi idanuwanta na sauka akan fuskar da bazata taba Mantawaba a zamansu na Greece ta bude Baki cikin wani irin slow tace

"SALEEM ZAD......

wani mummunan pause kafafun dad da Maheer sukai

Ammar dayake tsaye gefe idanuwansa ne suka fara sauka akan saleem din bayan Falaq cikin wani irin shock shima ya furta

"SALEEM ZAD"
#mamuh
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 69

*_ZUZEAM VENTURES_*
Best kayan Mata
08144015291

*NEW ALERT*
*END OF DISCUSSION PACKAGE*
~25k~ promo 12k
Barka da Sallah promo pack
1. Tabajen kankana da fruit
(Mai saukar da niima nan take ta kara miki dadi na musamman keda oga sai kunyi kukan dadi ranar )
2. gumbar chakwala dadi
(Hmm yar uwa daga jin wannan kema kinsani basai anbaki labariba wannan hadin na zallar dadi ne da ciko da gaba)
3. Turare kyauta dole
(Wannan turaren na amsar kyauta ne ina masu fama da miji mai mako wanda ba a cin kudinshi Ga shi da abun amma ba a ci to yar uwa matsalarki tazo karshe da izin Allah Sai kinci abunshi ina yan kasuwa duk kina amfani da wannan turaren sai Kinga budi da izinin Allah)
4. Zumar bata gaban kishiya yar asali
( wannan zumar Ga mata wanda kishiya ta shiga gabansu mijinki baki gane kanshi ya fifita yar uwarki akanki baya son mu'a mala dake ko wadda mijinta ke biye biye yar uwa kukanki yazo karshe duk kikayi amfani da ita duk machen da yayi sex da ita zaijita salab kamar dusa don haka aji tsoron Allah banda wanda suke zaune lfy da kishiyoyinsu)
5. End of discussion powder
( wannan garin karshen zance kenan hajiya oga ya taba miki kukan agwagwa ko mussoshi 😁to ranar duk da kika sha wannan hadin garin hajiya sabbatu sai kin rufe mishi baki ihu da kururuwa ba sauki kuma garin wata 7 yake ajiki yana aiki )

Hajiya karki bari wannan promo ya wuceki 25k ne promo saboda sallah 12k kacal

TikTok: Zuzeam.ventures5
Instagram: Zuzeam_ventures
WhatsApp: 08144015291

*********
Gabaki daya kowa sakin kowa yayi suna juyowa zuwa inda motar take Saleem Zad na tsaye ya fito sanye da black Armanis da suka fiddo asalin haskensa na zaadens sosai hutu, nutsuwa da kwanciyan hankalin dayake rayuwa acikinsa duka a bayyane tattare dashi.

Jannah da Bata shiga shock ne sosai ba ta sake ambatar sunansa tana isa gurinsa da gudun gaske ta fada jikinsa ya dauketa yana qanqameta Shima cikeda kewanta na ya kwanakin da yayi bayan rabuwansu idanuwansa Kafe akan Dad da Maheer da Ammar da suka kasa motsawa sbd tsananin shock.

Dad kafewa yawun bakinsa sukai kaf idanuwansa suka bushe yana Jin kaman mafarki ne yake yi Wanda yana kyafta ido zai zama ba gaskia ba Dan haka ya kasa kyafta ido bare motsawa

sbd yayiwa saleem dinsa kallan tsafta me Kyau.

Maheer Kuwa tsananin bugu zuciyarsa keyi yana kasa yadda da Saleem dinsu ne suke gani a gabansu sbd babu ta yanda Saleem zai bayyana a 4&4 a cikin motar AZIZ.

Ammar numfashi me karfin gaske ya saki yana takawa a hankali ya nufa Saleem din yana kasa dauke idanuwansa daga kallansa sbd a cikin familynsu bayan Mimi Saleem ne mafi kusa dashi Wanda kusancinsu yafi na kowa da shakuwansu da kaunarsa daban take a tsakaninsu.

Saleem sakin Jannah yayi yana takowa suka tsaya gap da juna shi da Ammar suna kallan juna kaman zasu hadiye juna sbd tsananin kauna da kewa ya bude Baki yana kallan Ammar din yace

"Dan uwa,likitan Mimi.......

Wata irin runguma Ammar ya Kai Masa me karfin gaske yana bude murya sosai da karfi yana furta "alhmdllh ya Allah"

Saleem dinma cikin tsananin farin cikin Jin Dan uwansa a jikinsa ya fara yiwa Allah godiya yana rungume Ammar din Shima yana Jin kaman zai tsaga zuciyarsa sbd farin ciki mara misali.

Maheer na ganin hakan ya tabbatarda Saleem dinne a gabansu dan haka cikin wani irin farin cikin da suka manta yanda yanayinsa yake a zuciya ya nufi Saleem din Wanda Shima ya nufosa shi da Dad ya hade ya rungeme suka shaqi qamshi juna take Dad ya fara wani irin kuka mara sauti yana Jin baqin cikinsa da quncinsa na duka duniya yana yayewa ganin 'dansa daya tak daya rage baya taredasu ya bayyana garesu bayan sun cire Rai daga sake ganinsa a rayuwa sbd tinanin bayama duniyar.

Shi kansa Saleem qanqame mahaifin nasa yayi yana hawaye masu zafi na radadin kewa da rayuwa me tsayin da sukai basa tare tareda gwawarmaya da kowannensu ya fuskanta ta rayuwa.

Su Ummah da Mama da sauran kowa zuru sukai suna kallansu cikeda murnan bayyanar Saleem din Wanda kusan kowa yasan waye shi hadda Ummah da batasansaba amma tasan sunansa a bakinsu Dan haka kowa zubarda makaman yaqinsa yayi suna Jin dadin komaima zai sassauta inshallah.

Sakin juna sukai saleem na kallan kowannensu cikeda farin ciki suma duka kowa ya kasa dauke idanuwansa daga kansa har lokacin kaman a mafarki suke Jin rayuwansu ya juya inda Ummah ke tsaye bayan Dad kamannin AZIZ da Falaq na bayyana akan fuskanta ya zuba mata idanuwansa yana kallan macen data haifi AZIZ LIMBA dinsa Kuma take a matsayin uwa a zaadens sannan Kuma matar mahaifinsa daga karshe Kuma uwar data haifi Ummitah mahaifiyar Falaq.

Takowa yayi ahankali ya tsaya gabanta idanuwansa na Dan sassauta kallansa akanta sbd girmamawa ya bude Baki a natse yana Bata girma da mutuntawa me girma ya bude Baki yace

"Ummah?

Murmushi Umman tayi tana Jin dadin yanda ya ambaceta da tsananin girmamawa da mutuntawa.

Gaidata yayi ta amsa tana Masa barka da dawowa ya juya gurin Mama wadda ke kallansa itama ya gaidata ya juyo gurin Fi dake kallansa cikeda murnan dawowansa sbd tinda suka dawo Nigeria basuyi magana ba a waya.

Akan Falaq ya tsaida idanuwansa wadda ke kallansa itama tin dazu tana mamakin bayyanarsa bayan ko a safiyan yau din sunyi magana ta chat bai fada mata yana ma Nigeria ba bare bayyana a gidan.

Dauke idanuwanta tayi daga kallansa tana qin ce Masa komai hakama bata bari yayi mata maganar ba ta koma gurin Jannah tana riqe hannuwanta tanajin idanuwansa akanta amma taqi ko dagowa bare kallansa.

Babu abinda Saleem din yace ko tsayawa dogon bayani kawai mota yace su shiga su tafi kawai.

Gabaki dayansu sun kasa hada tinaninsu daidai sbd bayyanar Saleem din duk ta qarasa juyar musu da Kai Dan haka motan kawai suka dunguma suna nufa a matse dasu bar gidan Dan sanin duk inda AZIZ  yake yana gap da shigowa.

Falaq ce ta sake riqe hannun Jannah tana girgiza mata kai akan kada ta tafi pls ta bari Daddynta ya dawo.

Su Dad da suka shige mota kokarin fitowa Maheer yake Saleem ya dakatar dashi da cewa

"No bara na gani"

Gefen Jannah din Saleem ya tsaya tareda Kafe Falaq din da idanuwansa zaiyi magana ta hanasa ta hanyar fashe Masa da kuka kawai na haushinsa datake ji Dana rashin son tafiyan Jannah din ya kalleta da sauri yana dawowa gefenta tareda Kai hannunsa kan nata dake riqe da Jannah ta fizge hannunta da karfi tana cewa

"Jannah bazata tafi koina bafa,
Matar Daddyna ce anan gurin zamanta yake a tareda mu,
Ba zata tafi tabar Daddyna ba bayan ga babynmu a tareda ita,

Idan ta tafi bazan sake ko kallanka ba"

Da mamaki Saleem din ya Kalli Falaq din da sauri kukanta na shigarsa daman komai kuka take Masa bare yanzu datakeyi da gaske batason Jannah ta tafi sbd Daddynta zai shiga damuwa.

Numfashi ya sauke yana kallan Jannah wadda take Jin idanuwan Dad da Maheer Kafe a Kanta ya bude Baki zaiyi magana Jannah din ta katsesa ta hanyar zare hannunta tana juyawa zuwa motar.

Da tsananin sauri Falaq ta yunkura zata sake kamota ba zato taji an riko hannunta ta baya tareda janyota jikin nutsuwa yana rungumeta jikinsa batareda yace komaiba.

Dukkaninsu babu Wanda ya lura da dawowansa bare isowansa gurin sbd tin a harabar gate din farko akai parking da motar sbd yasan daman Falaq zatai rigimar shiyasa ya kasa nutsuwa ya dawo hakama bai taba tsammanin Jannah din zata iya tafiya batareda nema ko sanar dashi ba duk da yasan inda zasu tafin amma ita batasan Saleem na zuwa daukansu ba.

Kowa wuta ya dauke ganinsa ba tsammani Dan haka su Dad suka fara kokarin dauke kallansu daga bangarensa sbd kada ma a tada maganar komai.

Su Mama Kuwa magana suke jiran yayi amma ga mamakin kowa saleem kawai ya kalla cikin nutsuwa yace

"A sauka Ify"

"Thank you B" Saleem ya fada yana kallan fuskansa da yake Karanto abubuwa da dama amma AZIZ din ya hanasa tirsasa kowa Dan haka juyawa yayi ya nufi motar.

Jannah dataji isowansa Kuma tasan yana bayanta dakatawa tayi ahankali tanason juyawa amma Dad da Maheer sun Kafeta da idon karma ta fara.

Kasawa zuciyarta tai ta juyo ahankali tana sauke idanuwanta akansa sedai ko inda take din bai samu damar kalla ba ya kama hannun Falaq suka juya zuwa ciki tareda su mama da Fi babu Wanda ya sake waiwayosu har suka shige.

Jin tayi zuciyarta na tsananin nauyi hankalinta na neman tashi Dan haka ta fara Ja da baya tana kokarin komawa Dan idan har Ummah zata zabi aurenta ta bisu itama bazata iya barin AZIZ ba sbd a zuciyarta tasan radadi da ciwo ne zai wadata.

Cikin sauri da karfi Maheer ya fito motar ya turata da karfi Dad na riqe hannunta suna kasa barin Saleem yasan meyake faruwa bayan motar take aka ja suka bar gidan kowannensu na Jin kaman ancire Masa wani nauyi a kirjinsa sbd samun yancin dena rayuwa a karkashin wani.

Magana sukeson yi amma wayar da Saleem keyi ce ta saka kowa yayi Shiru suna son sanar dashi basuda gurin zuwa bayan kauye.

Hanyar airport aka nufa Ammar na ganin hakan ya sake sauke ajiyan xuciya sbd babban abinda yake tsananin buqata a rayuwa yanzu daman shine barin Abuja kwata kwata rayuwansa.

Su Dad ma na ganin hakan take kowa ya fara Jin jikinsa yai sanyi sbd alamu sun fara nunawa Saleem ba Saleem na baya bane.

Suna isa kusan awa daya aka Bata gurin Shirin tafiyansu su dukan musamman muhammd da baa ga id card Dinsaba farko sai daga baya a cikin kaya Dan haka babu Bata lokaci ana gama komai suka isa cikin jirgi suka daga zuwa Lagos.

Muhammd ne bai taba shiga jirgi ba a cikinsu Fatma ta shiga sbd tafiyansu ta last time da AZIZ din Dan haka batai wani kauyanci ba kaman farko.

Zuru sukai dukkaninsu sbd gabaki daya sun cire Rai daga sake zuwa ko airport bare jirgi.

Har suka sauka Lagos babu Wanda ya isa magana sbd mamaki da Kuma zubawa sarautar Allah ido suga yanda Saleem din zaiyi dasu.

Mota biyu ta daukosu daga airport din zuwa gida,

Tin a security check point na shigowa anguwan Dad ya fara hawaye yana Jin tsikar jikinsa na tashi sbd yariga yaga rayuwar datake kokarin tabbata ta dawo musu.

Su Maheer ma gabaki daya jikinsu mutuwa yayi hawaye na ciko idanuwansu sbd harga Allah sun cire Rai da tsammani akan komawa rayuwar Jin dadin da suka rasa.

ZADs VILLA suka gani baro baro a rubuce jikin inda zasu shige suna shigewa ana parking Saleem ya fito ya fara budewa Dad mota kafin Ammar da Maheer ya kallesu cikin sanyi yace

"Welcome home Zaadens"

Rungumesa Ammar yayi yana fasa wani irin kuka Mai tsananin sanyi da Jin kirjinsa na sake sakewa ba nauyin komai sai sanyi da nutsuwa.

Dad da Maheer Kuwa qasa suka zube kafafunsu na mutuwa sukaiwa Allah sujjada suna yiwa Allah wata irin godiya kuka mara sauti na kufce musu.

Muhammd ma sujjadar yayi sbd yasan rayuwarsu suma ta gama inganta tako ina sbd sun Dade da zama zaadens din.

Jannah ma jikin Saleem din ta dawo gabaki dayanta a sanyaye zuciyarta ba dadi Sam bata Jin komai a ciki sai damuwa da tinanin AZIZ data kasa goge tinanin yanda ko kallanta ya kasa yi yayi tafiyansa da Falaq batareda yayi yunqurin hanata tafiya ba ko Hana a tafi da ita.

Ciki suka shiga masu aiki na fitowa suka kwashi kayansu wainda Kai tsaye store akai dasu sbd babu abinda baa gama jerawa a dakin kowaba na buqata komai an saka a dakin kowannensu hatta Muhammad dole an ware Masa nasa dakin daban Shima an zuba Masa dukiya lafiyayya.

Ba wani dogon Bata lokaci sbd ganin kaman ana cikin gajiya yasa kowa aka gabatar Masa da dakinsa ya shige hutawa da ganin sabuwar rayuwan da zasu fara.

Masu aiki Kuwa tini suka bada himmar hada abincin rana a kitchen sbd a kammala kafin kowa yagama hutawa ya fito.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 70

*_ZUZEAM VENTURES_*
Best kayan Mata
08144015291
*NEW ALERT*
*END OF DISCUSSION PACKAGE*
~25k~ promo 12k
Barka da Sallah promo pack
1. Tabajen kankana da fruit
(Mai saukar da niima nan take ta kara miki dadi na musamman keda oga sai kunyi kukan dadi ranar )
2. gumbar chakwala dadi
(Hmm yar uwa daga jin wannan kema kinsani basai anbaki labariba wannan hadin na zallar dadi ne da ciko da gaba)
3. Turare kyauta dole
(Wannan turaren na amsar kyauta ne ina masu fama da miji mai mako wanda ba a cin kudinshi Ga shi da abun amma ba a ci to yar uwa matsalarki tazo karshe da izin Allah Sai kinci abunshi ina yan kasuwa duk kina amfani da wannan turaren sai Kinga budi da izinin Allah)
4. Zumar bata gaban kishiya yar asali
( wannan zumar Ga mata wanda kishiya ta shiga gabansu mijinki baki gane kanshi ya fifita yar uwarki akanki baya son mu’a mala dake ko wadda mijinta ke biye biye yar uwa kukanki yazo karshe duk kikayi amfani da ita duk machen da yayi sex da ita zaijita salab kamar dusa don haka aji tsoron Allah banda wanda suke zaune lfy da kishiyoyinsu)
5. End of discussion powder

( wannan garin karshen zance kenan hajiya oga ya taba miki kukan agwagwa ko mussoshi 😁to ranar duk da kika sha wannan hadin garin hajiya sabbatu sai kin rufe mishi  baki ihu da kururuwa ba sauki kuma garin wata 7 yake ajiki yana aiki )

Hajiya karki bari wannan promo ya wuceki 25k ne promo saboda sallah 12k kacal

TikTok: Zuzeam.ventures5
Instagram: Zuzeam_ventures
WhatsApp: 08144015291

************

Kasancewan sun taso sun rayu a daula Dan irin wannan rayuwan ta hutu da Jin dadi da kwanciyan hankalin komai akwai na luxury rayuwa yasaka take suna samun kansu a cikinta a karo na biyu suka ji komai na baya ya dawo musu wata kwanciyan hankali na mamaye kansu da zuciyoyinsu daya saka zaadens din baya dawowa take amma a sabon yanayi da halayen da basa fatan na can baya su dawo musu.

Tsit gidan yai kowa na dakinsa babu Wanda ya fito sai bayan karfe uku na yamma tukuna suka fara fitowa daya bayan daya kaman yanda suka saba.

Muhammad da bai saba bane ya fara fitowa bayan ya gaji da duba komai na dakinsa daya bayan daya yana Jin wani irin yanayin da baisan ya zai fassaraba wai nasa ne komai dayake dakin,

Tarin shorts da singlets dake jere ya fara tsayawa yana mamakin duk nasa ne yayita sakawa kenan ake nufi,

Tinawa yayi da a baya kauye gajeran wandonsa daya ne tak Wanda duk ya dafe ya yage amma tinda ya fara rayuwa a 4&4 ya fara samun sauyin rayuwan dayake da shorts kusan Bakwai yanzu Kuma ga wasu kaya guda an Jere Masa.

Takarman da aka Jere Masa su kansu mamakinsu yakeyi Dan haka gayunsa sai Wanda ya manta tinda daman zama da Ammar ya koyi kwalisa da zama neat & clean.

Ya fito kusan so biyu amma babu Wanda ya fito Dan haka dole Shima ya koma ya kwanta baccin dole tinda dai yasan kila shi kowa ke yi.

Still shine ya fara tashi yayi wanka ya fito ya shirya cikin riga da wando coffee yayi Sallah yana idarwa ya fito yana qamshi me sanyi kaman ba shi ba Dan take yaga yama sauya shi Karan kansa din.

Yana zaunawa Palo Saleem ma na fitowa sai Ammar Wanda yake fidda kamshi me sanyi da

nutsuwa bayyane a fuskansa sbd bacci yayi lafiyayye ba damuwan komai yana tashi yayi wanka da sallah ya fito shima.

Maheer ne ya fito karshe kafin Dad Wanda yake kokarin Kiran wayar Ummah wadda tana sama tareda su Jannah a dakinta daban takuma kashe wayarta tinda tai waya da AZIZ ta sanar Masa sun sauka Dan haka Dad din ya kasa samunta.

Fatma data San kan gidan itace ta sauko bayan tayi wanka itama ta nufi kitchen ta saka hannu a aikin abincin da anriga an gama suka Jere a tare ta dauko ruwa da drinks ta jera ta koma ta hado fruits sbd Jannah ta ajiye ta nufi palo ta sanar dasu table ya zama ready.

Sama ta nufa ta sanar da Ummah kafin ta janyo Jannah wadda gabaki daya ta koma kaman ba ita ba babu farin ciki ko kadan a ranta.

A dining din suka zauna gabaki dayansu suka fara cin abinci Fatma ce tayi serving kowa tukuna itama ta zauna gefen Jannah wadda ta kasa cin abinci sai Dan tsakurawa takeyi kadan sbd batada appetite gaba daya.

Suna gama cin abincin babu Wanda yabar dining din Saleem ya sanar dasu komai gameda business dinsa da cigaban daya samu tareda dukkanin kadarorin da Zaadens suke dasu a yanzu sedai kaman yanda AZIZ yace bayason zaadens su San akwai saka hannunsa cikin farfado da sunan zaadens sbd kada su ringa Jin haryanzu a karkashinsa suke Dan haka bai fada ba yabi umarnin AZIZ din sbd su sake a cikin dukiyarsu hankali kwance ba tareda tinanin ta AZIZ bace.

Kowannensu yayi farin ciki Kuma sun so tambayarsa ya akai ya fita hannun AZIZ sai Kuma suka kasa sbd Ummah babu me son a sosa zuciyata ko kadan Dan haka suka bar zancen kawai tinda dai komai nasu ya sake dawowa garesu musamman shi Saleem din da suka samu ya dawo musu shine abinda yafi faranta ransu bama dukiyar ba duk da itama sun samu kansu a mafi girman farin ciki dawowansu akan kafafunsu da sunansu daya farfado ya sake tsayuwa a duniyar business dinsu.

Jannah data kasa cewa komai miqewa tayi tabar dining din ta nufi dakinta kawai ya rife tana kwanciyanta.

Fatma tattare gurin tayi tareda masu aiki tana sake komawa kitchen Dan ganin abinda yakamata a dafa na dare.

Ummah taso bin Jannah Ammar ne ya riqe hannun Umman yana Kallanta da kulawa yace

"Ummah ki barta tana buqatan time"

Dad dayake kallan Umman magana yaso yi amma Umman ta Maida hankalinta akan Ammar

tana magana dashi da Saleem tana kasa kallan ko inda Dad din yake sbd har lokacin zuciyarta sosuwa takeyi da abinda yace mata.

Fira da labarin baya suka zauna a palon sunayi har sallah tayi sukayo suka sake zaunawa har magrib tukuna kowa ya watse.

Daga masallaci acan su Dad suka sake zaunawa da saleem sukai Masa bayanin komai da ake ciki na cikin dayake jikin Jannah da hukuncin da suka yanke na riqeta tayi renan cikin har haihuwa.

Da mamaki Saleem ya kallesu Banda Ammar da bai saka bakinsa ba sbd yanzu ya iya tsayawa iya limits dinsa duk maganar AZIZ da Jannah ya dena shiga kwata kwata.

Cikin mamaki da damuwa Saleem yace

"Dad meyasa haryanzu Kun kasa yadda ku karbi AZIZ ne?
Idan har da gaske ne Kun cire komai a ranku Kun zubar babu sauran kowace irin tsana ko gaba to meyasa bazaku barsa da Jannah ba tinda gashinan clearly Kun gani tana sonsa haryanzu tinda ta iya Daukan cikinsa,

Dad kunsan wata ko satikan Jannah anan tareda mijinta?"

Da sauri suka kallesa da tsananin mamaki hadda Ammar Wanda koyaushe sabon mamaki yake samu gameda lamarin Jannah da AZIZ LIMBA.

Numfashi saleem ya sauke ahankali yana ajiye wannan zancen yace

"Dad ku Kalli ummah Dan Allah,
Ku Kalli yanda ta bar Dan data Haifa a cikinta sbd kawai tazo a cikinku tayi rayuwa kada ku shiga damuwa ko wani gararin sbd rashin uwa ko mace babba a familyn Nan,

Tanasonsa fiyeda kowa a duniya amma ta zabe ku akansa kunsan Yaya yake ji a xuciyansa amma ya danne ya hadiye ya yafe ta zo din sbd kawai yana tsananin son Jannah da girmama familynta duk da abinda ya faru a baya,

Dad pls Dan Allah ku barsu su samu farin cikin daya kamata sbd har abada Jannah bazata taba farin ciki da kowa ba idan ba AZIZ LIMBA ba haka ni kaina har abada AZIZ LIMBA bazai taba sauka ko raguwa daga zuciyata ba."

Yana gama fadan Hakan ya juya yabar gurin yana Jin gabaki daya familyn nasa sun sauya takaici da zaman gidan yari da garari duk ya yamutse kwakwalwansu.

Ammar ne yafara sauke ajiyan xuciya Shima cikin nutsuwa da sanyi yace

"Dad idan har sbd ni ne bazaku karban AZIZ ba wlh tallahi na Dade da cire Jannah a zuciyata sbd na riga na gani na tabbatarda har abada bazata iya son wani ba bayan AZIZ LIMBA,

Mune muka saka mata zuciyan datake bugawa a kirjinta Dan haka dole zamu hakura mu rungumi abinda zuciyar tazo dashi sbd zuciyar Ummitah bazata taba qin AZIZ LIMBA ba,Jannah da Ummitah ne suke tsananin sonsa a lokaci daya dan haka nidai na yafe na hakura na bar Jannah da Wanda takeso idan zaku yadda da Hakan mu taru mu rungumi abinda kaddara tazo dashi zamu Fi samun nutsuwa,

AZIZ LIMBA a zuciya yanzu ba maqiyina bane sbd har abada yanzu bazan iya qin jinin Ummah ba musamman da a gabansa ta zabe mu tabarsa babu amfanin dagewa akan aurenda masu auren suke son abinsu hakama bare Kuma AZIZ ya riga ya gama damu tinda ya dasa jininsa a cikinmu gwara mu rungumi kaddara mu rungumi abinda zaa Haifa shikenan"

Yana gama fadan Hakan Shima yabi bayan Saleem yabar gurin.

Muhammad ma bayan Ammar yabi sbd shine nasa aka bar Dad da Maheer tsaye a gurin babu me iya motsi ko cewa komai jikinsu a tsananin sanyaye sbd su kansu duk sun gaji da wannan masifar daga wannan sai wannan barema fada sukeyi a Baki sbd bacin Rai amma tsananin son da sukewa Jannah ko cikin shege ne a jikinta bazasu iya cirewa ba sbd kada wani abin ya sameta.

Da daddare Jannah Bata sauko cin abinci ba a daki fatma takai mata taci kadan Shima sbd zata Sha magani ne.

Karfe goma kowa ya shige jiki duk a sanyaye sbd yanda saleem ya sake nuna musu matsayin AZIZ LIMBA a rayuwansa ya wuce komai a yanzu Wanda Hakan yake musu nuni da ba riqon azaba ko wulaqantawa AZIZ yayiwa saleem din ba Dan haka sai sukaji kaman jikinsu na neman yin sanyi.

Washe gari dukkanin sauran abinda babu a Villa din na buqatan kowa Saida aka kawosa tareda wani irin sabon shopping din abinci da abubuwan buqata.

Haka suka sake wuni suna hutawa da sanin sauran abubuwan gidan Dana waje da anguwan Dan sanin inda zasu fara sabuwan rayuwa.

Kwanaki suka Dan fara dauka da dawowansu kowa ya fara kama harka gabansa,

Ammar fita yakeyi da mota shi da Muhammad sbd baida matsalar komai a ransa da damuwan Komai ya kwallafa ransa akan addua da yawaita karatun al'Quran da ummah ta tsaya tsaf akansa da Hakan Dan haka komai yaye Masa yakeyi kaman ba shiba.

Ummah ma hankalinta a kwance Jannah kawai take lallabawa sbd ganin ta kasa cire damuwa a ranta.

Shi kansa Saleem harkokinsa yakeyi hankali kwance sbd business dinsu gabaki daya dazai koma hannun Maheer sbd daman shine shigaban dayake gudanar dakomai da Zaadens,

Fatma ma hankalinta ya kwanta kwance batada damuwa ko matsalar komai itace take kulawa da komai na harka gidan duka masu aikin itace me fadan yanda zaayi sai Ummah wadda itace kaman shigaba kwata kwata.

Tsakanin Dad da ummah bayan gaisuwa babu abinda yake hadasu sbd Bata taba zuwa ko hanyar dakinsa ba tana sama ta tattarasa ta ajiye Da 'yayanta kawai take raharta da firarta sai Kuma AZIZ da kullum sai sunyi waya hankali kwance.

Dan haka hankalin Dad duk ya sake kasuwa Kashi Kashi sbd ya rasa ta ina zai fara kamawa,

Lamarin Jannah da AZIZ zai fara kamawa kokuwa na Umman wadda ko fuskan magana babu yanason Kuma magana da ita ya sanar mata cikin AZIZ ne a jikin Jannah.

Jannah Bata gama tsinkewa da shiga tashin hankali ba Saida taga suna maganar cike wata da dawowa Lagos amma ko so daya Bata taba Jin AZIZ LIMBA ba,

Bai taba nemanta ba,bai taba Kiran Fatma ya buqaci magana da itaba,
Koyaushe yana waya da Ummah tana jinsu amma bai taba tambaya ko yiwa ummah maganartaba,

Tsananin kewansa da damuwan abinda tai Masa ne suka fara nukurkusanta ta fara rama gashi anan gida ma kowa ya kasa cewa komai akanta kawai harkokin gabansu sukeyi har Umman taki ce mata komai akan AZIZ ko shiryasu kawai kulawa da ita akeyi da cikinta.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 71

Maheer daya fara zama busy hakama Ammar duk da Ammar bai shiga aikin sosai ba sbd yanayin lafiyansa dayake healing Amma dai da Muhammad suke zuwa ana koya Masa abubuwa da dama wainda zai iya duk da karatu Ammar din yake kokarin nema Masa ya fara.

Dad kuwa hutawa kawai yakeyi a gida Dan haka lokuta da dama shine da Ummah suke Kai Jannah din asibiti ganin doctor sbd yanzu baida zabin daya wuce Bata kulawa itada da cikin

dayake jikinta.

*******Sai da suka cike wata biyu cif da dawowa Lagos bata taba Jin koda muryansa ba hakama duk Kiran da zataiwa Falaq ko Fi bada taba yi Mata maganarsa Dan haka hakurinta ya qare ta da daddare bayan ta kwanta taji babyn cikinta na juyawa ahankali batasan lokacinda ta fasa kuka ba tana dafe cikin tana Jin kaman ta janyo AZIZ din zuwa garesu duk inda yake sbd suna tsakanin sonsa da kewansa,
Fushin dayake yi da ita kasheta yakeyi bazata iya jurewa ba yanzu Kam.

Kwana tayi tana kuka sosai Wanda ya a sakata tashi da zazzabi me karfin gaske.

Fatma ce ta fito daga dakinta ta shigo Dakin sanye da kayan baccinta riga da wando masu santsi.

Tana shigowa ganin Jannah a rife cikin bargo har lokacin ya sakata kallanta tana cewa

"Yaya dai?
Lafiya dai ko?

Qarasowa tai tana Dan zaunawa bakin gadon ta miqa Hannu tana Dan yaye mata bargon.

Wani zafi ne ya daki fuskanta da sauri ta Kalli Jannah din tana miqa Hannu a wuyanta ta taba taji zafin gaske.

Miqewa tai tana qarasa yaye mata rufar Jannah datake cikin tsananin azabar ciwon mara kuka ta fasa tana Jin kaman zata mutu jikinta na tsananin tsananin rawa ta qanqame cikinta.

A rikice Fatma ta fita ta nufi dakin Ummah taga Bata nan Dan haka ta sauko qasa da sauri tin a palo kafin ta isa hanyar kitchen take kwalawa Ummah kira.

Ba hayaniya a gidan Dan Hakan ne duk akai hayaniya a gidan koman kankantar ta saita damu kowa dan haka Muhammad ne ya fara fitowa sai Maheer Wanda yake Shirin ficewa sbd yanada baqin da zai gani a yau din.

Ummah dake kitchen daman lokuta da dama tana shiga kitchen ayi aiki da ita sbd motsa jiki,
Fitowa tayi tana goge hannunta da qaramin kitchen towel tana cewa

"Lafiya me yake faruwa ne kike wannan ihun Kiran"

Qarasowa Fatman tayi tana cewa

"Ummah ciwon mara sosai Jannah ke yi ko magana Bata iyawa ko haihuwa ce?

"Wace haihuwa ana zaune kalau ciki wata hudu cikin na Biyar"

Hanyar tafiya saman suka nufa hadda Maheer daya mara musu baya hankalinsa na Dan tashi.

Ummah na zuwa da saurin gaske ta isa gurin Jannah din wadda har ta fara Dan bleeding hankali tashe Ummah tace

"Maza asibiti zamu babba ne lamarin"

Maheer na Jin haka ya sauko yana cewa Muhammad ya fito da mota.

Kowa fitowa yayi take gabaki daya hankalinsu ya tashi Ammar ma fito da tasa motar yay hakama Saleem Dan haka Maheer ne ya koma ya daukota cak ya sauko da ita a motar Ammar ya sakata su Ummah suka shiga itada Fatma shi Kuma ya shiga ta Saleem suka bi bayansu zuwa asibiti zuciyoyinsu na sake tsinkewa.

Dad da Muhammad sai daga baya suka biyosu Muhammad yana tuqa motan Dad na kusa dashi.

Suna isa akai gaggawan karbanta zuwa ciki sbd zuwa lokacin tayi laushi sosai karfinta ya kare.

Tinda aka shige da ita kowannensu ya kasa zama zuciyar kowannensu na wani irin tsallen fargaba da damuwa,

Damuwansu da tsananin halinda suke shiga a baya ne a duk lokacinda aka kawo Jannah asibiti da tana ciwonta na baya ne ya sake dawo musu yana mamayesu sbd a yanzu dai gasu a tsaye ba zuciyar take buqataba halinda take ciki ko Rai dari nawa zasu kashe babu abinda zasu iya Bata ko mata a yanzu sbd magana ce ta wani Rai dayake motsi a cikinta Dan haka addua kawai da safa da marwa sukeyi zuciyoyinsu ba dadi.

A daidai wannan lokacin ne Kiran AZIZ ya shigo Wayan ummah ta Kalli wayar tana kasa dauka sbd batasan ya sani.

Har wayar ta tsinke Bata daga ba Dan haka yana sake wani kiran Bata daga ba ya dakata bai sake kira ba Dan daman iyayensa kawai yakewa kira biyu a rayuwansa,

ajiye wayan yayi kan table din abinci da suke Kai zasu fara breakfast daga gefe yana dagowa ya gaida Mama data ke isowa dining din.

Amsawa tayi tana zaunawa tace

"Kayi waya da Fatima kuwa sbd inata Kiran wayarta Bata dagawa tin daxu gashi Bata cika nesa

da wayarta ba"

Cikin nutsuwa da kamewansa yace

"Inaga tana wani abin Bata daukan Wayan kwata kwata"

Jin Hakan Falaq tace

"Bara na kira Jan muji ko Umman na wani abin ne to"

Wayan Jannah din ta saka kira da wayarta dake gefenta itama.

Harta yanke baa dauka Dan haka tana fada ko rife bakinta bataiba AZIZ ya dago tin kafin ya Kalli Sayd sayd din ya ciro wayarsa yana saka Kiran Saleem Zad sbd Jin lafiyan mutane biyu dayake dasu a zaadens babynsa da mahaifiyarsa.

Kiran Sayd na shiga wayar Saleem aka daga cikin sanyi da damuwan dayake kokarin daidaitawa saleem din ya sanar da Sayd suna asibiti da Jannah ba lafiya sosai she's bleeding.

Kallan LIMBA sayd yayi yana sallama da Saleem din ya kama nutsuwansa tsaf ya riqe kafin ya fara yiwa AZIZ din bayanin Jannah ce ba lafiya suna asibiti gabaki daya familyn.

A hankali cikin sanyi da nutsuwa AZIZ din ya sauke cup din dake bakinsa yana sipping lemon herbal tea ya buda baki yace

"Kasan meya kamata kayi"

"Already on it Sire" Sayd ya fada yana qarasa booking tickets din zuwa Lagos din.

Mama ce ta katse sayd din da cewa

"Am going too ka siya ticket Dani"

Cikin damuwa da neman fara kuka Falaq tace

"Allah yasa babu abinda zai samu baby limba da Jan,
Pls daddy nima zan tafi bazan iya zamaba,

Sayd na jin Hakan ya fara kokarin siyan tickets din dukansu kawai.

Nicky da kusan fiyeda kwanaki babu Wanda ya sakata a ido sbd kwata kwata Bata iya shiga mutane ce ta qaraso kunnuwanta na ji mata "BABY LIMBA" da Falaq ta ambata Wanda ya sakata tsayuwa daidai cikinta datake boyo yana bayyana a jikin hijabin da yanzu sune kayan

datake sakawa Dan boye cikin batareda ta sani ba shock ya sakata tsayuwa daidai cikin na bayyana akan idanuwan kowa muryanta ma rawa tace

"Cikin Jannah na AZIZ LIMBA ne ko me???

Mutuwan da kowa yayi zaune idanuwansu akan cikinta ya saka babu Wanda ya iya Bata amsa saima salati me karfi da Mama ta sake a rikice tana cewa

"Aysha Ciki ne a jikinki ko me??

Sai a lokacin AZIZ ya dago yana kallan Nicky din da mamakin maganar Maman sai gashi Kuwa idanuwansa suka ganar Masa ciki a jikin Nicky din.

Fiddausi data San da cikin Nicky Bata taba fada bane sbd rufa asirin da batasan Yaya yake ba amma tin kwanaki da dadewa taga cikin amma Bata fadawa kowa ba sunkuyar da Kanta tayi cikeda tausayin Nicky din wadda kowa ya kalli yanda take rayuwa yanzu yasan tana cikin tsananin qunci da kadaicin rayuwa da rashin kowa.

Falaq Kuwa cikin mamaki da tsananin tsoron daga ina ita Kuma Nicky ciki yake bayyana a jikinta?
Tsoro taji yana shigarta Dan haka miqewa tayi tana komawa bayan Daddynta cikeda mamaki me hade da tashin hankali.

AZIZ Jin yayi kansa yayi wani masifaffen nauyi hankalinsa na mummunan tashi ya Kafe cikin da idanuwa yana kasa yadda da ciki ne a jikinta sbd ba yanda zaayi tana amanarsa daya karba ta amininsa,likitansa daya zama shaqiqinsa wannan mummunan abin ya faru bai saniba sai dai yaga ciki kawai a jikinta,
To daga ina ma wai?

Bude Baki yayi idanuwansa na sauyawa zuwa Jan tsananin tashin hankali da bacin Rai zai ambaci sunanta ta yanke jiki a gurin tana faduwa sbd tsananin tashin hankali da tsoron cikinta daya bayyana a gaban AZIZ da damuwan data Dade tana cin zuciya da lafiyanta da rayuwanta ma gabaki daya batada inda take samun sanyi ko kadan.

AZIZ dinne ya tareta a jikinsa sbd faduwan da zatai a kife Da cikin a jikinta sai a lokacin hankalin kowama ya tashi da tsananin tausayinta sbd wata irin mummunan Rama ce ta bayyana a jikinta me muni da aka cire hijabinta.

Da sauri sayd ya fita yana janyo mota har kofar fitowa Palo
AZIZ dinne da kansa ya dauketa a jikinsa ya fito da ita idanuwansa na sake tsananta ja sbd wannan sabon tashin hankalin daya bayyana a ahalinsa Shima yanzu rana tsaka.

Asibiti suka isa da ita da gaggawa inda aka karbeta itama da gaggawa ana shigewa da ita.

Sai a lokacin ya zauna yana rintse idanuwa kansa na sake daukan nauyi yana shiga sabon damuwa da tashin hankali amma very calm yake a zaune bazaka ce yana cikin matsanancin damuwa da tashin hankali a cikin zuciyarsa ba.

Su Ummah ne suka iso asibitin itada Fi Banda Falaq da duk ta firgice sbd Bata taba ganin ciki da babu aure ba a zahiri duk Kuwa zamanta a turai da tashin ta acan.

Zaman jiran tsammani da damuwa sukeyi a gurin Fi nata kaida kawo tana Jin tausayin Nicky din na neman narka zuciyarta idanuwanta sai cikowa da hawaye sukeyi tana hadiyewa.

Ruwa Sayd yaje ya kawo mata ya kama hannunta ya zaunar da ita tareda miqa mata ruwan bayan ya bude mata cikeda kulawa da sanyin kalami yace

"Ki kwantar da hankalinki pls,
Babu abinda zai sameta zata tashi lafy kalau harma da babyn"

Zuba Masa idanuwanta tai tana Dan sake Jin kaman zatai Masa kuka ya lumshe Mata fararen idanuwansa yana gyada mata Kai alaman komai zai daidaita.

Ajiyan xuciya ta sauke tana Kai ruwan bakinta Tasha kadan ahankali tana miqa masa ya karba yana rufewa ya ajiye gefensa yana ciro handkerchief dinsa dayake fidda qamshinsa me sanyi da tsada ya Bata ta karba tana goge bakinta a hankali ta miqa masa ya karba yana maidawa aljihunsa yana sake kwantar mata da hankali sbd sanin abu kadan yake daga mata hankali.

Jikin Nicky din sosai ya rikice yana zama serious sbd ta jima bp dinta yahau sosai sbd tsananin qunci da damuwa da rashin kulawa Dan haka kwata kwata likitoci basu ga yanda suke so a tattare da ita ba Dan haka sukaita nuna rashin Jin dadin yanda aka kasa kulawa da ita sbd cikin aka bari damuwa da quncin sukai mata yawa.

Shiru AZIZ yayi damuwansa na tsananta sbd yanda yayi watsi da ita bai taba nema ko Jin lafiyanta ba ko Bata ko kallan rahama ne ko Dan sbd Dan uwanta da Kuma soyayyar datake Masa wadda ta sakata baro Dan uwanta da gatanta ta biyosu.

Hankalinsa rabuwa biyu yayi cikeda damuwa da dacin zuciya sbd nasa cikin na can cikin hadari hakama Nicky da Bata da kowa bayansu tana cikin hadari da nata babyn Wanda kafin komai ya biyo baya suna buqatan Bata kulawa da kokarin ganin ta tashi itama da nata babyn.

Sayd ne yayi duk wasu formalities daya kamata ayi na tafiyansu da Nicky din zuwa Lagos sbd hadewa a can gabaki daya Dan nema mata lafiya idanma waje ya kamata a fita da ita AZIZ din ya shirya Hakan sbd zai tsaya ya nema mata lafya da Jin damuwanta Dan debe mata kadaicin dake cin rayuwanta da Bata tarbiyan a Bata samu ba tin farko daman Hakan ya kamata yayi tin farkon zuwanta cikin iyalinsa bawai watsar da itaba da yanzu zuciyarta Bata lalace irin hakanba.

Cikin tattali da kulawan gaske ga mara lafiya jirginsu gabaki daya LIMBAS yabar Abuja zuwa Lagos.

A daidai wannan lokacin suma su modibbo dasu kawu motarsu ta sauka a Lagos Allah yayi sun taho ganin gida da hutu zuciyoyinsu fal farin ciki da tsananin murnan wannan arzikin daya tabbata dai anyi ana tareda su.
#MAMUH
07019691719*_KALBIM_*
Mamuhgee

Book 2
Chapter 72

Muhammad ne yaje park daukansu da lafiyayyar motarsa datake daukan idanuwansu suna ganinsa da farko basu ganesa ba sbd sauyawansa gabaki daya kwata kwata,

Ganin basu ganesa ba ya sakasa fitowa motar ya qaraso har gabansu cikeda farin cikin ganinsu da kulawa yace

"Modibbo barkanku da sauka"

Da sauri dukkaninsu suka sake Kafesa da idanuwa bakinsu na wata irin washewa da tsananin farin ciki da mamaki kawu isiya yace

"Garba,Garba Kaine kika koma haka kaman baturiya,
Garba ina Fatma itama ta sauya haka kenan??"

Murmushin nutsuwa garban ya sauke yana bude bayan mota ya saka kayansu yana cewa

"Kawu Fatmanku ai ta koma macen birni"

Wani sabon dadine yasake kashesu shi dai kawu jibo kallan garban kawai yakeyi yakasa dauke idanuwansa akansa yana Jin tsananin dadin 'dansa ne ya koma hakan,take yaji shi birni to tagama yi Masa komai ko ahakan sbd 'dansa ya zama me nasarar datafi ta kowa yaxo birni ya zaman Masa abin alfahari ba kaman sauran da suke lalacewaba idan sunxo su koma su zamarwa mutane abin kunya.

Motar suka shiga take wani sanyi da kamshi ya fara ratsasu suka fara Jin kaman dadi tin anan zai fara kashesu Dan haka suka hau tambayansa Shima yana tambayan mutanen gida da innarsa wadda yake jimawa baiyi waya da itaba sbd yanayin kauyen nasu.

Fira sukeyi sosai suna kokarin tambayansa adadin kudin da Zaadens sukai a yanzu sbd su San

abinda zaa basu tin yanzu.

Murmushi kawai yayi yana Dan juyowa ya kllesu yanda suka zuba Masa idanuwa dukkaninsu suna jiran amsarsa yace

"Modibbo babu ta yanda kowa zai San yawa ko adadin arzikin da suke dashi amma dai muna cikin arzikin sosai Kuma ku sani bawai maganar kudin da zaa baku bane ziyara kuka xo Kuma zaku samu lada me yawan datafi abinda kuke tinanin samu Dan haka Dan Allah modibbo kada kuyi maganar a Baku kudi ni kaina zan Baku ko nawa kukeso."

Shiru sukai dukkaninsu suna nazarin zancensa sbd shi kawu jibo a iya ganin da yayiwa garban nasa ma shi ko baa basa komaiba zai koma a Hakan sbd yasan dai 'dansa Shima yayi arzikin kansa.

Suna isa anguwan tin kafin su isa gidan su kawu ke kallan gidajen da suke sakasu rudani da lissafi sbd basu saba zuwa birni kaman modibbo ba dayake yawan zuwa Abuja.

Gate securities suka bude Masa yashigo yayi parking yana fitowa ya bude musu suka fito ya dauko jakar kayansu da tsaraban da sukayo ta kauye yayi ciki dasu suna biye dashi.

Akwai lafiyayyan Palo da Daki ta bayan nasa dakin Dan haka acan ya kaisu sbd bama kowa a gida duka suna asibiti duk da kowa yasan da zuwansu din shiyasa akace shi yaje ya daukosu.

Fatma daman kafin isowansu ta saka me aiki ta sake gyare dakin Dan haka suna shiga Nan ma kamshi da sanyin AC take yafara sanyayasu suka ringa Jin kasala suka zauna yana sake musu sannu da hanya.

Fita yayi masu aiki suka shigo da ruwa da drinks harma da abinci lafiyayyu aka fara jere musu suna gaidasu tareda musu barka da zuwa.

Muhammad dinne ya dawo yakai musu kayansu har bedroom ya Kuma kirasu ya nuna musu yanda zasuyi amfani da komai harma da toilet kafin ya nuna musu gabas ya fice Dan basu daman hutawa suci abinci suyi salloli.

Yana fita toilet suka fara shiga daya bayan daya sukai abubuwan da zasuyi suka zo sukai sallolin dake kansu suna gamawa suka fara bude abincin suna ganin yanda aka salwantar da rayukan kaji masu girma da tsoka kaman ba kaji ba take suka fara cin abincin duk da suna ganin plates din da aka kawo na cin abincin sun musu qananu sosai Dan haka kusan so uku uku suna ci kafin suka koshi suka cinye kajin tas suka cinye abincin Shima tas suka Sha ruwan sanyi da lemu masu sanyi take baccin gajiya ya daukesu ba jimawa ga AC dayake sake kashe musu jiki da kasala.

Muhammad asibiti yakoma ya sanar dasu isowan su modibbon suna gida suna hutawa.

Fatma ce ta koma gida sbd su modibbon da Kuma hada abincin da zaa kawo asibitin da Kanta.

Doctors sun samu dakatar da jinin dayakewa Jannah din zuba bayan tasha tsananin azaba tayi laushi sosai daqyar aka samu tsayar mata da babynta Wanda dukkanin zaadens babu Wanda hankalinsa baiyi mummunan tashi ba akan rasa babyn Wanda rashinsa zai tana Jannah hakama suma kasancewan babyn Jannah ne yasa suke tsananin kaunarsa a yanzu bama sa duba waye ubansa su a gani da tinaninsu babyn zaadens ne.

Samun nasarar tsayar da babyn yasaka zuciyoyinsu samun sukuni da nutsuwa suka samu kwanciyan hankali da farin ciki.

Dakin hutawa aka Maida Jannah din can sama wani private daki Wanda dukkaninsu suke zaune a sofas suna sake samun nutsuwa ita Kuma har lokacin bacci takeyi.

Saida aka tabbatarda komai yakoma daidai tukuna Dad da Ammar suka wuce gida Maheer m ya fice zuwa wani gurin aiki Mai mahimmancin da aka riga aka samu delay sbd tashin hankalin Jannah din.

Saleem da ummah aka bari Shima bai jima sosai ba ya tafi gida ya dawo.

Fatma data fara isowa gidan driver me ya kawota Dan haka kai tsaye gurin su modibbo ta nufa tana isa ta buga kofar Shiru Shiru sai tabude Kai tsaye taga bacci sukeyi ta fice tabarsu su huta tukuna sbd sun debo gajiyan gaske ta sani tinda tafiyan Mota ce.

Sama ta nufa dakinta ta fara yin wanka ta cire Dan warin asibitin data debo tai sallan magrib da akai ta sauko sanye da riga da skirt na atampa masu kyau da suka zauna jikin daidai Dan anyi musu dinkuna masu yawa da haryanzu basu ma saka wasu ba,

Kitchen ta nufa ta fara duba abincin da akeyi baa qarasa ba Nan ta saka hannu ta qara da dafa farfesun kifi da potato porridge.

Ganin kowa ya dawo gida sai ta saka aka jera komai a dining bayan tayiwa Ummah nata lafiyayyan basket din sai Kuma nasu modibbo daban da suma a daki zaa kaimusu.

Fitowa kitchen din tayi bayan ta wanke hannuwanta ta gogesu da towel ta nufi sama tayi sallah ta sauko tana nufar gurinsu modibbo.

Da sallama ta shiga sbd Jin magana Ashe basu kadai bane Maheer da Muhammad da Ammar harma da Dad duka suna dakin Dan haka cikin farin cikin ganinsu kyakkyawan fuskanta dauke da murmushi me Kyau ta fara gaidasu tana zaunawa gefen modibbo daya kasa rufe baki yana kallanta.

Kawu isiya Kuwa baisan lokacinda ya fasa kuka ba yana cewa

"Yanzu Fatma Dina ce wannan?
Fatma kece kika zama sarauniyar mata haka?
Fatma anya zan iya bawa shehu aurenki yana can yana jiran dawowanki"

Dariya Ammar yayi Mai qaramin sauti yana cewa

"Kaji Kuma wai wani shehu yake magana yanzu ana Zaune kalau"

Dad ma murmushi yayi yana cewa

"Fatma ai karatun zata fara yanzu kuma ai ba maganar aure tukuna saita gama ko nisa"

Muhammad da zancen ya basa dariya dariyar yakeyi sosai sbd yasan tin dama can Fatman bata son shehu.

Maheer ma maganar Dad ya maimaita da cewa

"Ai gwara ta gama karatun kwata kwata tukuna ma ayi maganar auren dan anayin auren zata iya watsar da karatun bare kuma idan shehun ne ai ba maganar qarasa karatu" ya qarasa zancen yana kallanta ta sake marairaice fuska tana kasa cewa komai sbd tanada Jin nauyi da sosai a gaban manyanta.

Cigaba da santin ganin yayansu kaman turawa su kawu sukai suna yiwa Allah godiya tareda zaadens din da suka riqesu da amanar gaske.

